Darajar Yayana3-01
Posted by ANaM Dorayi on 10:48 PM, 31-Mar-16
Under: DARAJAR 'YA'YANA
___________________NA
___________HALIMA K/MASHI
Gudu sosai Aliyu yake tamkar zaibar gari,zuciyarsa ta karaya gani yakeyi lallai yana dauke da ciwon har ya hangoshi kwance a rame ga kuraje sunyi mashi caba caba a jiki.da sauri ya ciro wayarshi ya kira layin likitan, Dr kana Asibiti ne? Dr ya ce eh, amma yanzunnan zan fita.Aliyu ya ce, don Allah ka jirani gani daf da Asibitinka.Sama sama suka gaisa, Aliyu yace likita ana yin gwaji yanxu a fitar da sakamako yanzu? likita ya ce gwajin mene?Aliyu ya ce, (H.I.V) ,Likitan ya zaro ido yana kallon Aliyu ranka ya dade kana zaton ciwon a tare da kaine?Aliyu ys ce eh likitan ya ce, likitan yace za a iya, da kansa yayi gwajin, ya daga ya nunawa Aliyu tare da cewa yanzu dai ya nuna baka da ciwon sai dai ba a gwajin farko ake tantancewaba.bayan wata uku za ayi wani, sanan in an sake yin wani wata ukun sai a sake gwadawa sau uku kenan,induk ya nuna babu to babu din kenan saboda gwajin farko yakan nuna babu kuma akwai.Aliyu ya lumshe ido, kenan likita yanzu bani da tabbas kenan? Likita yace gaskiya babu tabbas.ya dafa kafadar Aliyu cikin murya ta son kwantar masa da hankali ya ce, yallabai kadakadamu, ko da ya kasance kana da ciwon domin akwai magunguna wadanda masu ciwon suke sha duk karshen wata.sanan zakaci abubuwan gina jiki don karin kuzari, su magungunan suna yakine da kwayoyin cutar, suna hana kwayar ta karya garkuwar mai dauke da ciwon.Aliyu ya share zufar da ta keto masa ta goshi, sanan ya ce to nagode likitan ya ce se iyalanka ya kamata a gwadasu.Aliyu yakalli likitan yace ana iya daukar ciwon ta hanyar mu'amulan yau da kullum? kamar misalin ta hada kwanon abinci ko yin hirar fatar baki ne?likitan ya ce a'a Aliyu ya ce, to bana tsammanin suna da ciwon,kafin likitan ya sake magana, ya ce na gode likita, na barka lafiya.Da azama yafita ya

nufi gida.Nikam lokacin ina zaune bakin gado, idanuna banda xafi ba abinda suke yi, saboda kuka.hawayena sun daina zuba sun kafe. Nakosa yaya ya dawo, addu'a ta Allah yasa yaya bashi da ciwon, dama gidan bude yake dom haka sallamar shi kurum naji abakin kofa,Zubur na mike ina kallon shi, ya zauna bakin gado tare da sunkuyar da kai na dafe goshina ta re da cewa innalillahi wa inna ilaihi raji'un, yaya kana da ciwon ke nan? Shima da sauri ya mike tare da kama hannuna Sadiya kinatsu mana,nasoma kuka. Yaya ka cucemu, kila nima ina da ciwon, shike nan ka mai da mana yara marayu? Ganin yadda na rude yasa shi rumgumeni a jikinshi tsam.Saurara mana nima fa ba cewa akayi ina dashi ba. Na kalle shi me aka ce? Ya ce, sai anyi gwaji uku sanan za'a tabbatar amma yanxu ma ya nuna babu. Na sauke ajiyar zuciya, sanan na ci gaba da gunjin kuka ina cewa. Duk lokacin da bawa ya bar hanyar Allah tabbas sai ya fada da nasani. Aliyu ya ce kiyi hakuri mana Sadiya, nasan cewa ko da ta kasance ina dauke da ciwon nan, wlh sam nasan baki dashi, domin lokacin da na fada wanan kuskuren Allah ya sani ban rabeki ba sai yanzu na tuna ta iya yuwuwa baki da hakki ne shi yasa Allah yasa ban kusance ki ba. Nakalleshi idanuna jajur, tayaya kake zaton abinda ya shafeka bai shafeni ba? Naci gaba kaifa mijinane nasunna, ina sonka koda kai baka sona. Ya maza a ce abinda ya shafeka bai shafeni ba. Yace haka ne kiyi hakuri Sadiya. Tsam! namike nafada bandaki nayo alwala, zuwa nayi na fara jero nafiloli don neman sauki a gurin ubangijina. Can shima sai naga yayi tashi alwalar yazo ya kama yin nafilar, a hankali nake jin zuciyata tana sauka, danagaji sai na dauki alkur'ani littafin da ke dauke da waraka na soma karantawa. Munfi awa uku cikin wanan halin, lokacin zuciyata tayi sanyi kalau.

Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-

Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Shi yasa kullum ina alfaharin kasancewata musulma. Ina kara godewa ubangijin musullunci da ya kageni cikin wanan addini ya saukar mana da Alkur'ani don ya kasance waraka a garemu.Aduk lokacin da na karanta alkur'ani ko na saurareshi nakanji sauyin zuciya, ko cikin wata i ciiin matsala nake.Na kammala nazo na kwanta yanzu ina jin zan iya jure ko wacce iriin kaddara da zata hau kaina. Hakanan zan rufawa mijina asiri inshaAllahu, shima yazo ya kwanta dan nesa dani muna fuskantar juna. Ya ce kiyi hakuri don Allah kinji? Na ce, nayi hakuri, na yafe Abban Kausar, ya wuce a gurina na matsa kusa da shi. Ya ce baki jin tsoro na? Nace Abban Kausar mu bar wanan maganar. Ya rumgumeni, yau she rabom da na kwana hakarkarin mijina sai yau. Munso mu makara dan haka shine ya jamu sallah. Zan tafi kicin yace, dawo mu kwanta mu huta anjima ma karya na dawo muka kwanta Yadda nake jina yanzu ba zan juya masa baya ba. Har sai sha daya muka karya, sanan ya shirya ya nifi gidansu Iya ni kuma na shiga gyaran daki, minti shabiyar da fitar sa sai gashi ya kira, na daga tare da sallama. Cikin rudewa ya ce Sadiya kinga yaran nan sun hadani da Iya ko? Kuka fa na sameta tanayi please, kizo yanzun kitaimakeni sam taki saurarena. Hankalina ya tashi. Akofar gida na sameshi tsaye cikin damuwa nace meyafaru? Ya ce wlh ban sanme yarannan suka ce mata ba, na shigo na sameta cikin damuwa natambayeta me ya faru? Tana kallo na sai kawai ta fashe da kuka, wai naci amanar ta nasan dai maganar bata wucea kan matsalarmu dakeba. Ban san me zance mata ba, domin bani da yanda zan wanke kaina. Laifi dai nayishi, don Allah shiga ki bata hakuri, anjima zanxo da Usman neman tuba gurinta. Cikin hanzari na shige gidan, kan kujera na sameta cikin tashin hankali nazauna ina fadin Iya menene? Abban kausar yayi min waya wai inzo, ya ganki cikin damuwa. Sam idona ya rufe ban lura da su Kausar ba, sai da naji

muryarta ta ce, wlh Mami ni banibace nafadaba, Al'amin ne yace yasan yanzu kina can kina kuka, shine Iya taji tace kukan me? Shine mukayi shiru, ta ce mu fada nacemashi ni ba ruwana kin hana mu fada, shine ta tsaremu ta ce, zata zanemu, shine nace inmun fadamata kada ta fadamaki. Shine muka fada mata cewa kullum Abban mu in ya dawo sai ya sa ki kuka, yayi ta zaginki. Na kama musu kunnuwa, muryar Iya naji ta ce sakar musu kunne, in ba ke ma kinaso inyi fushi dake bane. Ni na san cewa wanan ramar taki akwai bakin ciki a cikinta. Wato dama gadanga cin amanar da aka bashi yakeyi? Shine ke kika zabi ki zauna ki hadiye bakin cikin da namiji kina kan kanuwarki. Sai yanzune kike cikin shekara ashirin da biyar, amma kika juri wulakanci. To ki sani ni ba xan yarda ba, ai kodanace in matsala ta taso kada ki nemeni ban ce haka dan kicutu ba, na furtane dan in tabbatar kina sonshi badole nayimakiba. Da naga ta nunfasa sai na ce Iya yaran nan karya suke yi, dan sabanine mukasamu kwanan baya, kuma mun sulhunta, dan Allah Iya kada kiyi fushi da yaya, ko mai ya wuce. Ta ce yaro da wuya yayi karya. Daidai lokacin yaya yasake shigowa,Iya ta dube shi Aliyu ina son ka sani,Sadiya bazata koma gidan ka ba, dan ba zan yardaba ace har yayanku sun san cewa kana cutar uwarsu ba. Shi yasa tun farko na ki batun auran, don nasan halinka. Hankalin yaya Aliyu yasake tashi, ya curo wayarsa ya kirawo Usman, ya ce dan Allah Usman kazo gidan Iya yanzunnan. Ba tare da ya jira Usman me zai ce ba, ya kashe wayar shi. Sadiya ta tsurawa su Kausat ido sam bata so suka fada wa Iya wanan maganarba.badon kar a rabata da mijinta ba, sai dan bata son Iya tashiga damuwa, musanman yanzu da ya kasance Iya batada koshin lfy. Iya ta ce, kun tsaresu da ido ne don sun fadi gaskiya? Na ce Iya yaran nan fa karya suke yi. Aliyu ya ce ba karya bane Iya, sai dai sunfada maki a daidai lokacin da muka shirya na san in Usman yazo zai gamsar da ke. Wasa wasa har Usman ya shigo Iya ba ta daina fada ba shi ma shiru ya zauna yayi

har sai da iya ta numfasa, sanan ya shiga bata hakuri tare da lallashinta. Ya tabbatar mata da cewa an daidaita, ta ce ina son jin wacce matsala ce ta taso har yarinya ta kode haka? Sanan in san wake da matsala? Muka kalli juna ni da yaya, Usman yace zai fi kyau Iya abin da ya wuce ya wuce muyi adu'ar Allah ya kare gaba. Ta ce sam sai fa ta ji menene ya haifar da rashin jituwar saboda gudun sake faruwar abin nan gaba dan ta san wane irin mataki zata dauka. Inko ba'afada minba to sai dai ya rubuta takardar sakin Sadiya ya bani. Kai Usman ai kasan ko mai, badan son raina akai auran nanba sabo da gudun haka, don haka yanzun ma bata baciba ya bar min 'yata. Aliyu ya ce Usman fada ma Iya komai duk hukuncin datayanke a kaina na cancanceshi. Nayi saurin kallon Usman, ko da wasa bazan bari Iya tasan ainihin abin da ya faru ba duk da na san Aliyu dan ta ne amma bazanso tajiba. Muryar Usman ce ta katseni, wato ainihin abin da ya faru....Nayu zaraf na katse shi gaskiya Iya ainihin abin da ya faru laifinane.Na kalli su Kausar kufita waje. Suka fita nasun kuyar da kai ina tunanin wane laifi zan dorawa kai na? Dama na ce ne bana so in sake hai huwa, yara uku sun isheni, shi ne yaya ya dauki gaba dani. Dakin yayi tsit, na fada haka ne dan nasan babu abun da iya take so kamar taga yayan ta suna haihuwa, na saci kallon ta ni ta ke kallo cikin bacin rai. Ta soma sabon kuka yanzu Sadiya ke ce baki son hai huwa? In baki haihuba me zakiyi? Wasu ma son haihuwar suke da kudi amma ba su samu ba, sai ke ishashshiya. Na soma hawaye don tausayin kaina, nazama kyandir in kona kaina don in haska shi, na ce Iya ki yafe min, domin shi ma yaya tuni ya yafe min. Na kalli Usman a gabanka aka yi komai ko? Usman ya lumshe ido, zuciyar shi cike da mamaki bai taba ganin irin Sadiya ba. Duk irin cutar da mijinta yayi mata amma ta yarda ta shafawa kanta kashi, don kurum ta wanke shi. Na danyi dim dan tsoron kada Usman yatona dan naga yayi shiru, na ce yaya Usman kuba Iya hakuri. Iya ce ta daka min tsawa da cewa, kada

ki damu mutane, kuma ina son ki sani wanan ya zama na karshe, in na sake jin wani laifi makamancin wanan zaki ga matakin da zan dauka. Ta kalli yaya Aliyu cikin taushin murya kayi hakuri Aliyu, inshaAllahu bazata sake kwatanta haka ba. Yaya Aliyu dai ya kasa koda daga kai, jikinsa kuma ya mutu.Zan mike ta ce ke zauna ban gama da ke ba,nakoma na zauna. Ya aliyu ya zuba min ido, sanan ya kalli Iya. Iya kada ki damu, ko mai ya wuce ta shi mu tafi. Iya ta ce kuje zatazo yanzun, suna fita Iya tace, na san cewa abin da kika fada ba shi bane ainihin matsalar ku ba, kilama kin fada ne dan ki wanke shi. Amna in haka ne da gaske ina mai yi maki nasiha ki jitsoron Allah, ki bi abin da mijinkike so, duk mutum na kwarai ba zai ki yin murna da kyautar da Allah yayi mashi ba. Koma menene zan ci gaba da yi maku adu'a, tashi kije. Na mike zaraf ta re da cewa, to Iya nagode, insha Allahu bazaki sake jin kan mu ba. Ta ce kuma kar inji kin daki yaran nan, gashi a ban za kin sa suna jin haushin mahaifin su, har suna fadin basu son yadawo. Na ce bazan masu komaiba. nakirasu muka fita.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com Kokuma ku kasance taredamu a facebook https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Usman ya kalli Aliyu bayan sunfita ya ce aboki in har ka sake cin zarafin matarka hakika Allah bazai kyalekaba. Dubi yanda ta dorawa kanta laifi don ta wanke ka. Aliyu ya ce, nikaina baka ga na kasa maganaba? Lallai Allah ya taimakeni Sadiya ta taimakeni, wlh kaji na rantse maka yau da Iya ta ji ko mai na kade, ba zankara kima a Idontaba. Sannan sai ta raba ni da matata. Usman ya ce, to sai kayi mata adalci tunda abin yazo da sauki. Da muka fito duk suka nufo gun mu Usman ya ce Sadiya Allah ya shi maki albarka,da'a ce mata da yawa suna da hali irin naki, na tabbata da aure da yawa ba zai mutuba.

Nakalli Aliyu, shima ni yake kallo. Ya ce my choice na gode, ina sake rokonki afuwa ki yafe min. Na ce ya wuce. Na tasa yarana muka tafi gida nazaunar dasu,Kausar nace yanzu kun kyauta kenan da kuka sa Iya kuka? Kausar ta ce Momy Al'amin ne. Na ce to kar ku sake, Al'amin ya ce, momy ba zan sake ba.
Ko daran ranar Aliyu banda hakuri babu abinda yake bani, duk ba wannan ce matsalata ba, ya ya za'a kare da batun (H.I.V) da kuma batun yarinyar nan? Don haka na waiwayo na dube shi daga inda nike kwance, shima rigingine yake idanunsa suna kallon sama. Tsakaninmu mutum guda zai iya kwanciya tsakaninmu, na ce ' Yaya! Bai amsa ba, na daga murya 'Yaya' shru, da alamu tunaninsaya tsawaita. Don haka na mike na kunna fitilar dakin,haske ya mamaye ko ina,na tsura mashi ido cikin faduwar gaba. Nagirgiza da ganin hawaye suna gudu layi bibbiyu daga idananun Yaya daya yamiko zuwa kumatu. Yayin da dayan ya bi gefen ido. A fili nafurta'Inna lillahi wa inna ilaihir raji'un! Yaya! Na kira shi tare d zama kusa dashi na kwantar d kaina a kirjinshi, kunnuwana suna jiyo yanda yake ta kokawa d kukanshi a kirjin. Ina zaton yana kokowar danne kukan ne, yayinda shi kuma kukan ke ta yunkurin fitowa. Da sauri na dora tafin hannuna a kirjinshi ina ta shafa kirjin, wai nufina in taya shi lallashin kukan. Bakina ya soma fadin 'Haba Yayana, me kuma ya faru? Tuni na yafe abinda kayimin, namaka alkawarin rayuwar da tafi wadda muka yi baya dadi. Sai naji hannunsa a gadon bayana, ya damki rigata d dan karfi alamun har yanxu yna ckin cikin kunci, muryarshi sarke cikin rawa irinta mai kukan baqin ciki. Ya ce, Sadiya ba anan matsalar take ba, Sadiya baqin cikina ciwon in ya kasance ina da ciwo..." kasa karasawa yyi don kukan da ke son subuce masa. Nace Yaya ko kana da ciwon nan zan zauna d kai,ko banidashi zan yarda ka sa min. Nima kukan ne ya kufce min,cikin kukan na ce 'Yaya zan zaunada kai haka ina sonka." Sosai ya rungumeni tsam "Sadiya ba zan cuce ki ba, bayan Allahya tsare ki,nikuma

nine nacuci kaina, domin duk wanda ya bar dokar Ubangijinshi ya dauki son zuciyarshi, ya saki koyarwar Abul Kasim, Manzonmu mai tsira da aminci, ya bi ta Yahudu d Nasara to bako shakka karshenshi nadama da kuma danasani, lokacin da ba su da amfani. Sadiya lokacin da shaidaniyar yarinyar ta ziyarce ni da ban bi son shaidaniyar zuciyata ba duk da haka bata faruba. Ba ina kukan ciwon da kila zai zama ina da shi bane, ba ina kukan ci gaba da rayuwata ba ne ina kukan yanda zan bar ki da wahalar jinyata da dawainiyar yarana. Sannan kukan abinda da zan tarar a cikin kabarina ban san me zan gaya wa Ubangijinaba, Yayi shru cikin shassheka, nima kukana ya qaru. Nace, Yaya inshaAllahu bakadashi, ka ci gaba da neman gafarar Ubangijinka, Allah mai amsar tuban bayinshi ne.Ya yunkura ya tada mu zaune ya dago fuskata muna kallon juna ido cikin ido,ya ce 'Sadiya ban makara ba ko? Na girgiza kai, Baka makara ba Yaya. Ka daina tunanin cewa zaka mutu ka bar ni,insha Allahu kai ne wakilin gawata,kai zaka fara binne ni Yaya. Ya rungume ni tsam a kirjinsa tamkar ya buda kirjin ya saka ni. 'Ina sonki Sadiya,ina son yarana,ina son iya. Amma haka nan in ta kasance zan barku...... Wayarshi ta katse maganarsa, tamkar kada ya dauka don ji yake komai ma ya tsara shi rayuwarshi ta kare. Ni ce na dauko wayar na mika masa, Adewalene direbansa na can, tamkar kada ya daga na ce'Yaya ka amsa mana.' A kasalance ya yi sallama,Ade ya amsa sannan ya ce, 'Oga dama madam ce a Asibiti ba lafiya,shine take tasa aka dauki lambata a ka kira ni. Me? Naji Aliyu ya furta da karfi, 'Mujidat ba ta da lafiya?? Nima gabana ya yi wata mummunar faduwa,tamkar ni ce na daga wayar. Idanuna waje ni ke tambayr me ya same ta? Aliyu ma da ya rasa me zai fada sai ya maimaita tambayar da nayi. 'Adewale meyasame ta? A can bangaren Adewale ya amsa da cewa, shi fa bai sani ba,amma ga ta bari ya bata. Aliyu cikin daga murya ya ce,kada ka bata,bana son jin muryarta,macuciya. Na yi

saurin fadin 'Yaya a bata wayar mu ji daga bakinta, da gaske tana da ciwon? Shiru Yaya yayi yana kallona,hankali tashe bayn ya katse wayar. Na ce Yaya don Alla ka kira a bata mu ji, ba don son ranshi ya kira ba,sai don na nace da cewa ya yi hakan.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
A handsfree ya saka ta, Ade ya daga ya ce bata,murya can kasa ta ce 'Hello' ya katseta da cewa,'Kiran ubanme kikace amin? Na fada miki bani bake, kuma ina Allah ya isa da sanin da na yi miki,macuciya.Dama kin san cewa kina da (H.I.V) shi ne ki ka like min sabida ki cutar da ni da Iyalina? Wani kara ta saki mai karfi tana fadin 'A'a, a'a ni ba ni d (H.I.V) sai dai in kai ne kasa min. Muka kalli juna ni da shi, ya ce 'Yanzun wane ciwo ki keyi dazakice baki da (H.I.V)? Tace, 'Ina dauke da cikinka ne yana wahalar da ni,amma bani da (H.I.V)....' Ya katseta da karfi Cikin tsawa cikin masifa take fadin 'Kada ka sake zagin ubana,wannan cikin naka ne ban taba yarda na bi wani ba tare da abin karyar cuta ko ciki ba sai kai daya danike So. In ma (H.I.V) ne kaika samin kamar yanda ka sa min wannan cikin,kuma ina sonka sani ba zan taba cire shi ba,zan haifi dan soyayya,zan zo har garinku gurin danginka don su san kana da da' ko 'ya da ni. Haka nan masoyiyarka da ka yi min wulaqanci sabida ita,ita ma ya dace mu san juna. Duk da tsawar da yake daka mata bata yi shuruba,sai data kai aya. Ni kam baqin ciki ya hana ni magana,sai hawaye. Na mike zan fita,ya riko min hannu tare da finciko ni na fado jikinshi,ya kashe wayar yana fadin. 'Haba Sadiya, ina ce murna zamu yi tunda ba ciwon gare ta ba? Na mishi wani kallo tamkar in hau shi da duka,cikin zafin rai na ce 'Ba gara ciwon ba da cikin da ka yi mata? Yanzun me ka shirya fadawa danginka in

ta zo musu da da'? Ya ce, ki barta bata ma isa ba ne,taje can ta nemi Uban cikinta. Ya tausasa murya. 'Na rantse miki bazan karbi cikinba, kibarta zan nemi transfer in bar garin ba shienanba. Yayi ta lallashina ina kuka, ya yi ta tsara min zantuka har nayi shiru,amma sam naki magana, ga ciwon kai tamkar zai rabe. Ya jawo ni jikinshi 'Ba kincekin yafe min ba? Na dafe kaina tare da fadin 'Wash Allah na.. A rude ya tambayeta "kan ki na ciwo ne? Na daga kai alamun 'Eh"ya kawo min panadol ya ba ni na sha. Haka ya yi ta ririta ni da lallashi tare da maganganun kwantar da hankali har bacci yadaukeni. Shi kuma ya mike ya shiga sintirin kai kawo dakin, daga bisa niya dau ki wayar shi ya nufi can harabar gidan, dan kada ya tashi wani daga cikin iyalin sa. Yanzu ya fi shakkar yaran sa, domin ya fahimta lallai in yayi wasa zai sha mamaki dasu. Layin mujidat ya kira, ringing na uku ta dauka Aliyu yace, na kirakine in gargadeki, kiyihanzarin fita harkata, kuma ki nemi uban cikinki, ni ba nine uban sa ba. Dama karuwa tana da miji ne da har zata sami uban da? Ta soma kuka, tana cewa kaine ubansa, kabidani ta lalama in ba haka ba zaka ga yanda ake iskanci. Kana kirana karuwa kai ya sunan ka? Gara ma kazo cikin satin nan in ba haka ba za ka ganni a Kaduna. Aliyu ya ce dole zan dawo tinda gurin aiki nane, amma ki sani babuke, zai fi maki sauki ki zubar da wanan cikin tunda baki tuna ubansaba... Mujidat ta katse shi ina zaton baka sanni ba ne shine yasa ka ce haka, amma zan nuna maka kalata. Kuma bazan zubar da cikin ba, wanan cikin shine ya zo min dai dai lokacin da nake bukatar shi zai tai maka min sosai. Wanan cikin shine zai hana rabuwar mu ni da kai, kasani mun hadu har abada . Ta katse wayar.

Ranar da zai koma tamkar inyi me don ta kai ci, nasan dole sai sun hadu da yarinyar nan ga ciki. Shi kanshi tunda akayi batun cikin ban sake ko dariya ba, ya lura da hakan. Da zai tafi sai min dadin baki yake gaskiya ni fa Abban kausar gara

min ace daga ni har kai muna da ciwon kan jamau da batun cikin. Nan ya rike min hannu, don Allah ki saki ranki ki aje maganar yarinyar nan a gefe, ke kiji a rankima an
shafe babin ta a bayan kasa, kinji don Allah. Na ce hum! Shi ke nan Allah ya saukeka lafiya. Ko da ya sauka yana ta kokarin yawan kirana da sauransu. Nakula sosai yana son shikam lallai sai mun koma tamkar da, nima dai ina ta kokartawa don ganin anyi hakan duk da ina tsoron mai zai biyo baya kan batun yarinyar da cikinta.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Aliyu da yake zaune a bayan motar sa ya dubi Ade wale da ke tuki ya ce masa kasan gidan da Mujidat take? Ade wale ya ce a a sai dai gidan yarta yasa ni inda ya taba kaita sai ko asibitin da ta kwanta. Aliyu ya daga waya ya danna mata kira, har ta katse bata daga ba. Ya shareta da farko amma sai kuma ya tuna yana son kwarai su tattauna abu mai mahman ci. Don haka sai ya sake daga wayar da nufin kiranta, amma sai ga kiranta ya shigo, cikin sauri ya daga. Ta ce kamar kana jiran kira na? Aliyu ya ce ko daya ina dai yunkurin kiranki ne. Tayi yar dariya. Ashe dai ka damudani? Yace ke bankiraki don naji salon zancekiba, inaxan same ki? Ta sake yin yar dariya da ya tsana a yanzun, ka bari ni nasan indazan sameka,tunda ka shigo garinnan nasami labarin zuwanka, sanan ka manta nice na kiraka ba kai ne ka kirani ba da har zaka ce bakakirani dan kaji salobane. Ya katse ta, ki fada min inda xan same ki yanzu nace,tasake yin yar shewa tare da fadin ashe dai har yanzu kana tare dani, ni nasan tunda ka shigo dole ka neme ni ko dan cikinka. Cikin fushi ya ce, kar ki tsamma ci cewa haduwar mu zata haifa maki da mai ido, ko kusa ganina bazai farantamaki rai.... Ta katse shi da cewa, in ji wa? Ai ko zaka kashe ni ganinka ya fiye mun

komai farin ciki ko kasan ina sonka fiye da mahaifana? tayaya zan kasa farin cikinganinka? cikinhaushi yace Amma kin yi asara tunda baza ki fadin in da kike ba bari in koma gida Cikin sauri tace ina Hotel din Hamada Daki na sahashida,ka iso Ify masoyina Tsaki yaja sannan ya katse layin sannan ya kalli direba muje Hotel din Hamada ko cikin harabar hotel bai shiga ba Aliyu yace ya tsaya ya sake kiran layin ta ta daga tare da fadin bude ka shigo mai sona yace ke shashasha fito ina can bakin gate sannan ya katse bai tsaya jin me xata ce ba sanye da dogowar bakar jallabiya da dan kwalinta sai takalmi baki mara tudu sam yanxun baya ko son ganinta don haka ya daure fuska tamkar baitaba dariya ba sam,yanxu baya ko son ganinta don haka ya daure fuska tamkar in ya bude baki xai fito da wuta don hada rai, tana isowa saitinsa ta nufa don tasan gurin xamansa yasauke gilashin tana kallonshi gabata ya fadi amma sai ta dake saboda iya bariki tace maigidana ina son in ganka cikin iri kamewar gaskiya kada kace aikinka kafito mushiga ciki ya yi mata kallon banxa tamkar yaga kashi sannan yace shiga mota muje tace ina? tace. sai kinji? Tace bari in dauko jakata yace (cikin tsawa ) in kin koma ciki ni kuma zan fi cikin sauri ta zagaya ta bude mota tana fadin gida zamu je kenan? ko tanka ta bai yi ba yace Adewale sai da ya harba motar kan titi sannan yace Oga. gida zamuje? Aliyu yace babban asibitin garin nan zamuje ta zaro idoda sauri tace yin me? ku tsaya in sauka bazanbikuba ,tasoma lalube zata bude kofa Aliyu yace bazan hanaki ki fita ba amma ki sani in ki fado kan titin nan ba lallai ne ki rayu ba wanda hakan ba zai dameniba yan uwanki ne za su yi rashi,ta dan shiru tana tunanin me zatayi don kuwa itakam bazata taba yarda a cire mata cikinnanba Don tasan shi ne kadai abinda ya rage mata wanda zata rike Aliyu da shi dole ya saurare ta ta kalleshi nifa bana son ka kai ni a cire min ciki ya dubeta. ina ruwana da cikinki bashi ne matsalata ba ta sauke ajiyar zuciya tare da jingina kanta a jikin kujerar mota ta tabbata

gaske ne ba abinda zai kaisu kenanba ta sake kallon shi me zamu je yi ya dauki wayarshi yana naiman wani layi ya karata a kunne tare da fadin in mun je kyaji,Suna shiga dakin ganin likitan wanda ya riga ya shaida masa yana tafe, ya baiwa likitan hannu suka gaisa. 'Yan sanda sukan saba da likitoci sbd yanayin ayyukansu, don haka Aliyu yasan likitoci da dama a Asibitoci daban daban. Ya nuna Mujidat gata nan, Mujidat ta soma zare ido, sai dai ganin Likitan ya dauko kayan gwajin (H.I.V), sai ta kwantar da hankalinta dan tasan bata da shi din amma Likitan ya ba da lokaci wata uku nan gaba su dawon a sake gwadawa, ya umarta shima a gwada shi. Sakamakon dai duk daya ne, babu, Aliyu zuciyarshi yanzun ta nutsu d cewa bashi da (H.I.V) ya yi wa liktan godiya sannan suka yi sallama. Suna fitowa ya shiga motarshi. Direba zai tada kenan tazo ta bude zata shiga. Aliyu ya ce, (cikin tsawa) 'karki shigo min mota, sannan banida buqatar sake ganinki a rayuwata.' Ta ce, 'Labari kake yi'. Ta dafa cikinta, 'in kai danka ina? Kai ba ka san bala'ina ba ko? Za ka sha mamakin abinda da zai biyo baya in har ka ki tsayawa mu sasanta, Mujidat kawai ka sani amma ba ka san halinta ba. ya daka ma Adewale tsawa, 'Muje mana, 'Take ya figi mota suka yi gaba in da har Mujidat ta ku san faduwa, kofar motar ta rufe gam! Suka bar ta a nan. Ta bi motar da kallo cikin kunan rai, a fili ta ce 'Wannan bai sanni ba, bai san yana cin albarkacin so bane? Amma zai san ya kirama kanshi ruwa.' ta nufi titi don hawa acaba.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Tun lokacin d muka samu sabani d Yaya Aliyu,kusan ko yaushe dakin yarana ni ke kwana don samun sauqin wasu abubuwan, ko na ce tunane tunane. Yau ma niyyata kenan inna gama

can zani cikinsu in kwanta, zan fita dakin kenan wayata ta soma ruri. Na koma kan gado na kwanta sannan na daga tare da yina sallama. Ya Aliyu ya amsa,sannan ya ce 'My choice Alhamdulillah.'Na ce, 'Shin ne abin godiya. Ya ce, 'Ina mana murna gaske yarinyar nan ba ta da (H.I.V). Na lumshe ido cikin jin dadi,amma sai na tuno d cikinta, na ce 'To cikin fa? Ya ce, 'Ina ruwana d cikinta, ban bi ta kanshi ba, don ba matsalata ba ce,' Nace, 'Matsalarka ce, tunda kwanka ne. Babu yadda za'a yi mace ita daya ta dauki ciki. 'Raina ya soma zafi, ya ce 'Ni kadai nayi hulda d ita?? cikin bacin rai na ce 'Amma kai ka ajeta a gida.' Kuka ya subuce min, sai na kashewayar nayi jifa da ita na ci gaba da kuka. Inaji yana ta sake kira amma na qi dagawa, inna tuno wai Aliyu shi ne ya yi ma wata ciki, abin nan yana soya min rai. Duk ranar d aka kawo mana dan me zai fada ma duniya? Mezai fada ma zuri'arshi? Musamman yaranshi masu wayon tsiya? Banji bude kofa ba, sai dai muryar kausar naji tana cewa, 'Momi wanene? Da sauri na share hawayena ta ce, 'Momi Abbanmu ba ya ce kun daina fada ba? 'Na ce, 'Jeki dauko min magani, kaina ke ciwo na kasa tashi ne. Da gudu ta fita, saiga ta da shi har da ruwa. Ina sha ne naji sakonni suna ta shigowa cikin wayata,na bata kofin na ce 'Kije ku kwanta, kiyi muku addu'a zan yi waya da Abbanku. Ta ce, 'Momi kin fasa yi mana tarihin d ki ka ce za ki yi mana na rayuwar Manzon Allah? Na ce,'kin ga kaina na ciwo,sai gobe.
My choice ki bari mu sake daidaita kanmu, ki bari mu saita rayuwarmu, ki amince da ban hakurina. Tsaki naja sannan na duba dayan sakon.
Kin yi alkawarin cewa kin yafe min, kamata yayi ki mance kmai,ina sonki my choice, kece rayuwata.
Na sake jan tsaki a fili na ce, 'Kamar gaske. Wani sakon ya sake shigowa.
Don darajar Allah da girmansa d darajar lokacind muka kasance a baya, d martabar soyayyarmu,ki amice da ban haqurina. Amicewarki kurum shine

daga wayata , xan kira ki yanxun . Dagawarki itace zata tabbatar min cewa kin hkr.
Na ajiye wayar tare da yin rigingine na kumaruntse idona, matsalata ina da rauni da sanyin zuciya, bugu da kari ina son mijina.Bana jure in wulakantahi, tausayinshi na daga cikin abinda ke sa in kauda kai ga abubuwan da yake min...ringing din wayarsane ya dawo dani tunanina. Na dauki wayar tare da yin sallama cikin makoshi , yace"ngd da daga wayata, yanxun na yarda kin yafe min.Inason mu koma kamar da, yanxun ki fada min abinda kikeson muyi. Nace kamar me? Yace wlh bana son bacin ranki ne, shine nake son ki tsara mana yanda zamu shimfida sabuwar rayuwa, wadda baza ta katse ba."Nace kamar gaske, kila sai kasa na soma farin ciki daga baya ka canza min. Allah sarki Sadiya sarkin son soyayya, sai gani ina 'yar dariya, nace duk Ikcn da ka so. Shima yayi 'yar dariya.Inzo gobe? Nace koh yanxu ma ka zo. Yace insha Allahu ranar jumma'a xan taho, roko nike ma Allah yasa suyi min transfer zuwa arewa.Nace amin yace ina yarana? Nace suna dakinsu sunyi bacci. Yace, to bari in amsa waya xan sake kiranki.Ba'a fi minti dayaba ya sake kirana yace zan fita barayi ne a cikin wani kauye, shi ne aka kira ni yanxun. Nace Allah ya tsare. Nayi birgima a kan gado, zuciyata fes. Wata zuciyar tace lallai ke dai sakara ce, duk irin abinda mutumin nan ya kunsa miki shinecikin mintin da bai kai 10 ba har kin manta?Nadan yi tsai ina son inyi tunani, tabbas xuciyata shagalalliya ce ma'abociyar son a sota, da zaran abin son ta ya fuskance ta sai ta bude da yawa ta shiga cikin farinciki.Idan abin sonta ya juya mata baya sai ta shiga kunci ta tsuke , ta dinga zafi. Nayi murmushi tare da rungume filo, a fili na furta.Allah kakauda shedan tsakanina da mijina. kullum yanxn ina cikin farinciki sbd xan kira yaya a Ikcn dana so, kuma shima yana kirana, sannn ga hirar kwantar da hankali tare da ban baki da yake min kullum.Tun ranar Alhamis naje gidan kitso na kuma biya gurin mai zana

fulawr dayis tayi mana har da Kausar da Mama.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Tun safiya Jumua'a na hana kaina sakat da ayyuka. Funkasau na kwaba sai kuma farar shinkafa, nayi kunun zaki na sayo fura.Duk abinda nasan yanaso haka na tanade shi, a wayarmu ta karshe baifi saura minti hamsin ya isoba don haka na feshe yara nima na saka kayan da bai sanni dasu ba, a sunan Aisha na dinka su, atamfa ce blue mai ratsin yellow. Ina jin kwankwasa gida nace su Kausar Abbanku, maimakon su biyo ni kamar yanda da can mukeyi, sai naga duk sun tsaya.Kausar ma hade rai tayi, na kamo hannunta,kuzo muje mu taro shi. Biyo ni sukayi , na bude gida jan gwarzo na yau cikin kakinsa yake, ya aje jaka muka rungume juna cikin murna da doki.Muka kalli yaranmu lamarin ya zame musu tamkar sabon abu.Kausar ma rufe fuska tayia lamun kunya.Al'ameen ne ma naga yana tadariya. Muka kalli juna ni dashi , ya sakeni yaje ya rungumi Kausar, sannan Al'ameen da ya aje shi ne ya dauki Maama ni kuma na kwashi kayansa muka nufi ciki.Tamkar da ya basu leda dauke da kayan ciye ciye tasu tsarabar, nan muka barsu faloya shiga wanka, kamar da nice na taimaka masa yayi wanka.Tsaf ya shirya muka fito gurin cin abinci, yanda yaran suka ganmu har sun soma sakin jiki, abinci kam ya rasa da wanne xai soma.Ya kamo hannuna yana yabon lallena, kausar dake can gefe tace Abba nima kaga nawa, harda Mama akayi mana . Yace , iye! 'Yan gata kunyi kyau yarana, nayi kasa da murya ina cewa Kausar fa hankalinta yana kanmu. Yace, duk zatonta yau ma rigimar zamuyi? Nace wannan ya zama tarihi. Muka sa dariya, daya kammala ya mike.Dauko hijabinki kuzo mu fita. Yara suka hau tsalle muna gaba ni da yaya, su kam suna baya.Gidan iya muka soma

zuwa, muka bata tsarabarta. Sai gidan Usman nan ne ma muka dan dade.Sun kama hirar siyasa ni kuma muka kulle da Anty Abida cikin daki, shawarwari tayi ta bani kan cewa kada in sake inyi fushi ko in dauki gaba da mijina don yana bin mata.Yin haka zaisa ya kara zakewa.tace kin ba shi dama kenan, amma in kika jawo shi kika ninka abinda kike masa ada, kika hada da addu'a sai kiga komai ya daidata. Nace bakisan wani abuba Anty, yanzun yarinyar tana da ciki, ko Usman bai fadawaba, abinda ke batamin rai kenan, kuma tasha alwashin sai ta haife dan cikinta ta kawo shi.Anty Abida tayi salati tare da rike baki tace lallai akwai matsala. Nace nayi nayi ya tsayamuyi shawara ni da shi amma yaki yace in bar zancen. Tace shikenan tunda baya son zancen ki kyale shi, Allah ya rufa asiri, nace amin. Daga nan yayi ta yawo damu supermarket da stores kalakala. Mun kwaso kayan ciye,ne da suturu da takalma, ni kama har da mayafai da jaka. Gsky ranar ya kashe mana kudi, haka muka shigo gida nikiniki da kaya, yarana nadade sosai bangan su cikin farin ciki kamar yau ba. Lallai rashin jituwar iyaye ba karamin shafar rayuwar yara takeyiba. Don Allah iyaye in wata matsala ta gifto muku ku daina sa'insa gaban 'ya'yanku, don gudun lalacewar tarbiyyarsu, tare da jefa rayuwar su cikin rudani,Tun daga ranar dayace min yana tafe nayi ta hada abubuwana ina sha , yanxun ma zumata na samu na kada kwaina na hada na shanye.Sabon wanka nayi na saka sabuwar rigar baccin daya zaba in a fitar da mukayi, yanxun na kama gashina shi kam yana falo yana kallon labarai a tashar Aljazeera,Yara tuni sunyi bacci, ban fito ba nima sai nabi kan gadona na fada tsakiyar gadon nayi kwanciyata.Da zai yiwu in bada labarin daran ranar kila da nan zan kare, domin ya shiga sahun tarihin da ba zai gogu ba a zukatanmu.A cewar yaya, daran ya dara na farkonmu.Da safe mun tashi tamkar sabon aure, cikin kwalliya muke aiki tare dashi a kicin. kwanaki biyun da Yaya ya yi sai da na rubuta su cikin dan kundin adana mahimman sirrikana. Da

zai tafi har kuka nayi. Allah sarki rayuwa,mun koma tamkar da har mun fi da kyau,rayuwar aure d zaman lafiya gami d soyayya akwai dadi. Tuni Aliyu ya mantar da ni abinda ya faru a baya. Kuma ko na tuna bana jin haushi,don na dauke shi matsayin jarabta. Sai dai fa duk lokacin da na tuna cewa wata tana can dauke d cikinsa ina tsorata da abinda zai biyo baya. Kwatsam sai ga shi anyo ma Yaya transfer zuwa Abuja.mun yi murna don ganin Abuja ni ke tamkar kaduna, tunda ya koma nan ba ya jimawa bai zo ba. Wata rana har can Abujar ya kan tafi da mu muyi hutun karshen mako. Rayuwa dai ta jin dadi muna ciki. Kwatsam wani yammacin ranar Talata ina tsakar gida ina kwashe shanyar kayan makarantar yara da na wanke. A jikina ina sanye da doguwar riga mai hade da hula blue da ratsin fari,sai naji ana buga min gida, na nufi kofar ina tambayr kaina ko wa ye?? Ina budewa muka hada ido da ita, gabana yayi mummunar faduwa. Ina zaton ko cikin duhu na ganta zan gane ta, bare a haske,domin na sha ganin hotunanta cikin facebook, tana sanye d doguwar riga ja hade d mayafinta. Sannan tana janye d akwatinta, ga wata ta rataya a kafada. Na dake na sake dubanta. 'Malama daga ina? Kuma wa ki ke nema? Ta ce, 'Nan ne gidan Aliyu Tukur jami'in dan sanda? Na ce, eh nan ne. 'Sai naga ta turo kai, na ce 'Ba ki minbayani ba kina kokarin shige min gida. Tayi min wani kallo sama da kasa, 'Ni bakuwarshi ce, Allah yasa yana gari? Na maida kofar na rufe,tare d cewa 'Bayanan yana Abuja, lafiya? Ta nufi ciki. Zo ki nuna min inda zan zauna, a gajiye nike, don na wahala kafin na gano gidan. Falo na sauketa duk da tafasar da zuciyata ke yi, amma na danne har ruwa na bata. Sannan na zauna na kalle ta. 'Baiwar Allah daga ina ki ka zo neman Maigidana? Ta gyara zama 'Ciki ya yimin,ta fada a gadarance ba tare d jin wani nauyi ko shakka ba, ni kuwa duk da cewa nasan batun sai da gabana ya fadi da jin furucinta. nace, 'Ciki? Ta ce 'Eh, shi ne don wulaqanci ya ci moriyar ganga zai yada

kwauronta? Bai isa ba. Sai yasan ya taba annoba. Raina ya soma daukan zafi a gurin,na daga waya na kira shi,ringing din farko ya daga tamkar yana zaman jiran kirana ne. Ya ce,'Ya ya dai my choice? Don in nuna ma Mujidat ban damu ba, na ce 'Sweety kayi baquwane,da sauri ya ce, Daga ina? Na kalleta tamkar ban san ds batunta da shiba, na ce ya ce daga ina? Ta miqo hannu 'Ba ni wayar. 'Nayi 'Yar dariya. Ke ba ki d wayar ne? Fadi kawai daga inda kike in sanar dashi. Cikin son ta tura min haushi ta ce, fada masa wadda yayi ma ciki ce. Kalmar tana dukan kirjina in ta furta, amma na dake na ce 'Wai wadda ka yi ma ciki ce. Na karasa zance da dariyar bakin ciki. Da sauri ya ce, 'Mujidat? Subhnllhi! Lallai wannan 'yar iskar tana son jaza min bala'i ne. Ta ya ya ta gano gidana? Na tabe baki tare da cewa, 'Oho' ya ce, 'Kai wannan akwai 'Yar iskar yarinya. Sadiya don Allah kiyi hakuri kinji? Zan taho yau din nan kmai dare, amma yanzun ya ya za'a yi? Na ce, kaika san yanda za ka yi da ita. 'Ya dan yi shiru yana nazari, duk a rude yake,ya ce, 'Sadiya. Na ce, 'Na'am, 'Ya ce, 'Kuna tare ne yanzun haka? Na ce,'Eh. Ya ce, shiga daki muyi magana. Na ce, To. Na miqe na nufi daki. Na shige Toilet na rufe, sannan na ce 'Ina jin ka. Ya ce, 'Sadiya don Allah kiyi hakuri kwakwalwata ta toshe, ki buda min ita ya ya za a yi yanzun? Raina bace yake matuka, na ce 'Lokacin da za ka yi sabonka ka nemi shawarata? Don haka sai ka nemi shedanin daya hure maka kunne ya sa ka a hanyar da za ka warware matsalar. Ya ce, Sadiya duk ba wannan zancen ba, yara na gida tayi magana? Na ce, 'A'a suna islamiyya. Ya ce, 'Ok, yanzu yaya za ayi? Na ce, 'Wallahi ban sani ba, ni dai bani da dakin da zata kwana sai dai in dakinka. Ya ce, 'Zan taho yanzun nan zansa jami'an tsaro su kulle min ita. Na ce, 'Kana ganin wannan mafita ce? Yarinyar nan irin 'yan iskan nan ne ma su tutiya da iskancinsu. A shirye take d ta shelanta ma duniya ita farkarka ce, kuma tana da cikinka.ka shirya zubewar mutuncinka? In ka shirya ka zo ka bi ta d zafii in ko kana son

tsira d dan ragowar mutuncinka,to koka tabbata za ka bi ta ne da lalama ka kuma yi mata adalci tunda lokacin daza ku yi shedanar ba ka juyamata baya ba. Na kashe wayar tamkar in yi kuka, amma sai na fasa don bana son wannan Mujidat din ta fahimci abinda ta zo dashi ya daga hankalina. Ko kuwa ya dadani da kasa,don na lura 'Yar bariki ce.nasame ta inda na barta sai dai yanzun ta dan kwanta akan kujerar. Na dube ta 'ya ce ki jira shi yanzun zai baro Abuja,kina buqatar wani abu yanzun? Ta ce, 'A'a bana jin yunwa na ci abinci a gidan cin abinci. Na wuce na ci gabad aikina sai dai kunci da takaici a zuciyata ba a magana.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Shida daidai yara suka dawo Islamiya kallonta suka dinga yi sannan suka gaishe ta. Ta ce yara masu kyau,ina kausar?Ta ce, 'Gani. Mujidat ta ce, Yar lelen Babanta duk ya fi ambatar ta cikin yaran. Kai ne Al'ameen? Ya ce, 'Eh. Ta ce, 'Ka yi min kyau, kana kama da babanka sai ka shiga raina. Ta dubi Mama ta yatsina fuska, 'Ke ce mai kama d mamnki ko? Sunfi ki kyau, Allah yasa babyna ya yi kama da.............'' Da karfi na daka mata tsawa 'Ke! Mahaukaciyace? 'Na kalli su kausar, ku je dakin ku ku cire kaya ina zuwa. Na dubeta bayan shigarsu daki,mekike shirin fadawa yarana? Kina so ki fada musu kina da ciki da babansu? Ta 'Eh ai dole su sani ko da ban fada musuba, domin a gidan nan zan haife shi. Na runtse ido don baqin ciki na bude tare da furzar da takaicina ta baki, na ce ba zan hanaki ki haihu a gidan nan b, sai dai zan gargade ki kar ki sake ki fadawa yarana maganar data fi karfin tunaninsu, kin gane? Ta yi 'Yar dariya,sannan ta ce, Bani da magana dake bare ki sa min doka, mijinki nake jira. Haushi ya turnikeni har na kasa tsaida shi na ce, 'Mijina fa nawa ne kar ki ga na

miki tarbar mutunci ki za ta shakka ce, in na ga dama ba ki ganin mijinnawa, sannan dole ki bar min gidana. Ta saka dariya, sannan ta debi kafafunta ta zuba kan kujerata kuma kallona sama d kasa,sannan ta ce.........zandakata anan, zakuji zarar Allah yanufa..
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Zaharaddeen Shomar
Whatsapp  08168575100

Darajar Yayana3-03
Posted by ANaM Dorayi on 12:12 AM, 04-Apr-16
Under: DARAJAR 'YA'YANA
___________________NA
____________HALIMA K/MASHI
Assalamu'alaikum,akaro na barkatai gani na dawo domin kawo muku cigaban labarinmu ,fatan kuna sane da inda muka tsaya.
Yayi shiru. Na ce Hello, kana jina? Eh, kin fadawa Iya ne? Na ce, nanmuka amshi haihuwar tare, Kasan cewa taso ta gano cewa danka ne? Dan yaron yayi kama da kai fiye da duk yaran gidan nan.Da karfi yace Haba dai! Wlh, yaushe zaka zo? Yayi dan tsaki, gaskiya bani da ranar zuwa, zan turo miki kudi kiyi duk abinda ya dace. Nace, zuwan ka yana da muhimmanci, sabida Mujidat zata iya tana komaifa, inbata gankaba. Ya ce, to zan zo kafin suna inkuma dawo
Gurin aikina. Nace to saikazo. Na kira auntyAbida na fada mata, haka ma Aisha kawata.Makota duk suna ta shigowa Barka. Su kausar ma nasa sunje sunga baby,na fada musu cewa kaninsune, suna ta murna har da kausar. Aisha ranar datazo barka tana daukan yaron tace, kai Sadiya yaron nan yana kama da Abban kausar. Nace, haka ake

ta cewa, dama kin san mutane sun ce in mai ciki tana yawan kallon mutum ta kan haifi mai kama da shi. Ta yi Yar dariyar yake,tare da cewa, hakane kawata.Mai jego kam ina kallon ta sai harara take watso mana. Muna shiga dakina tace, Sadiya anya kuwa ba kanshin gaskiya a cikin lamarin matar nan? Kin san halin mazannan ko dai Dan sa ne? Ki yi hakuri kamarce naga tayi yawa. Nace, hum! Ke dai bari kawata, tsakanina dake nasan amanace, wlh dansane ciki yayo mata, yanzun data haihu zasuyi aure. Aisha amana na fada maki ko iya bata San wannan ba. Aisha ta zabura tare da fadin, kan uba! Lallai Sadiya ban taba sanin cewa Ke sakarya bace sai yau, yayowa wata ciki sannan ki yarda ta zauna maki a gida? Wallahi da ace nasan haka ne in nazo barka shegiya nake,kin ma daure masa gindi kenan gobe ya kara.Na ce, Aisha ki fahimta, uban 'ya'yanane,mijina kuma yaya zanyi? Nawa ganin rufin asirinshi Nawa ne, kuma na yara nane. Ta yi tsaki bana Jin zan fahimceki, in tazo gidan ta koreki kin ga ai sai kiji dadin rufa masa asirin. Na ce, nasan dama bazaki fahimceniba, shi yasa tun farko ban sanar da Ke ba, dan na sanki. Ta dauki yarta tasa a baya,ta suri jakarta da hijabinta, Ni kin ga tafiyata. Na bita ina fadin, "Dan Allah Aisha ki saurareni. Ki tayi ta tafi abinta. Na ce to shi Kenan in kin huce za muyi waya ta ce ni kar ki kira ni. Na dawo daki na kwanta kan gado ina hawaye, in na tuno Yaya zasuyi aure da Mujidat Abin na daga hankalina ya kuma sani kuka. Ranarr da suka cika kwana 5, sai ga Yayakusan 10 na dare, Ni ce ma na bude masa kofa, ya janyo ni jikinsa,ni kaina bansan me yasa jikina yayi sanyi ba kuma banyi wani farinciki da ganinsa ba. Ya dago fuskata, sannan yahaskani da wayarsa, lafiya my choice? Na sa hannu na tare hasken,lafuya mana Yaya mai ka gani? Na karbi jakar hnnunsa tare da cewa sannu da zuwa,bai amsa ba sai dai ya ce, na ganki cool ne, kamar ba kiyi farin ciki da gani na ba. Na ce, bacci na fara. Sannan nayi gaba na bude masa daki ya shiga. Ya zauna bakin gado tare da fadin, na gaji

yau Sosai,8 ta wuce na baro Abuja, kuma da safe zan wuce na zone Kawai sabida kin nuna zuwan nawa yana da muhimmanci. Na ce, to Kayi wanka zaka warware. Ya ce to. Kafin ya fito wanka na kawo masa tuwo daman shi nayi a daren miyar zogole. Sai da yaci na fitar da kwanukan, sannan na shiga gurin Mujidat tana zaune da waya tana chatting, na ce, ya kamata fa ki dinga bacci. Ta ce, ba zan yi hira da kawayena ba? Na ce, kuyi tayi, akawo yaro babanshi yazo. Ta kalli yaron sannan ta kalleni, ya yi bacci. Na Isa gurin yaron na dauko shi, ban tsaya jiranta ba na kai shi. Aliyu ya mike tsaye zumbur likacin da ya kalli yaron duk yadda Sadiya Ke bashi labarin kamannin shi da dan bai zaci har hakaba. Ya kalli yaron kusan minti 1, sannan ya miko mini tmkr yana tsorace,na maida hannuwana baya. Kayi masa addu'a kamar sauran yaran ka duk dadai baka samar da shi ta hanyar da shari'a ta amince ba, sannan ka yi masa hudu ba,ya daga murya rikeshi mana Sadiya. Na juya na fita. Abin mamaki sai ga Mujidat labe tana lekenmu, na tsaya turus ina kallonta, ita ma ta yi tsuru-tsuru na ce, a'a dama kina min labe? Ta soma Sosa kai, sai kuma ta shiga borin kunya, kin zo kin daukarmin yaro ba dole inbiba? Na ce, kina zargin zan cutar miki da yaro ne? Yaya ya fito ya mika mata yaron "ungo yaron ki kar ku tada min da yara suna bacci. Ta amshi danta ta tafi, ni kam a gurin na tsaya na ma rasa tunanin da zanyi, tun yanzu kenan kafin a daura Auren? Shi kam bai so yanda ya yi ba kada ma mu tada masa yara suna bacci, maimakon ya gargadeta kan cewa Kar tasake yi min labe, bai yi hakan ba sai ya shige abinsa. Ni kam dakin yarana na nufa amman ko zama ban yi ba sai ga kiranshi, sai da wyrta kusa tsinkewa sannan na daga. Meyene? Yace, zomana,sai da na dan bata lokaci, sannan na je. Kai kawo na samu yana yi a cikin dakin, ina shiga ya nufo ni ya kama hannuwana. Sadiya asirin da muka rufa zai tonu sabida kamannina da yaron nan ya dauko,ina ganin gara mu fadawa Iya Kawai ita kuma Mujidat ta yi tafiyarta tunda

dama dan Kar Iya su sani ne zan aure ta, ni wallahi bana son ta, zata iya tarwatsa min iyali,na zame hannuna daga nasa na zauna bakin gado tare da rike kaina na ce, Yaya ba dan Kar asirin ka ya tonu Kadai ba ne na ce ka aureta, don gudun kada kuci gaba da haihuwa a titi babu aure, don nasan bazaku rabuba. Shima ya zauna, sai dai in itace baza ta rabu dani ba Sadiya, amman wallahi ni tuni na barta,na girgiza kai, Yaya yin Aurenku yafi a kan barin shi, don Mujidat ta tabbatarmin da hakan kuma na San zaku iya... hawaye suka soma zubomin cikin rawar murya na ce. kuma duk laifin kane. Ya kwanto ni jikinshi, wallahi Sadiya nayi nadama matuka, kuma naji kunyarki Sosai ki yi hakuri kidaina kuka, Kecefa kike Karfafa min gwiwa,kike bani shawara. Ya dago fuska ta. Hankalina yatashi da yawa ganin kamannin yaron nan,nasan sai dai mutane su ji mu Kawai, ammababu wanda zai yarda cewa ba yaro na bane. Ya share min hawaye. Ki yafe min. Na ce, Yaya ni dai alfarma Kawai zan roka a gurin ka guda biyu. Da sauri ya ce, na miki alkawarin yi miki su fadi inji.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com Kokuma ku kasance taredamu a facebook https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Na ce, na farko duk rintsi kada ka juya min baya ko ka wulakanta ni. Ya rike kafaduna muna kallon juna, insha Allahu Sadiya ba zan miki ba ko bisa kuskure insha Allahu. Nace sai na biyu, izini zaka yi min in nemi koyarwa a makaranta, ko L.E.A ta nan unguwar Mu'azu. Ya yi shiru yana nazari, can ya ce, kin gane Sadiya ba wai ina son hanaki bane, nafison ki nutsu a gida wallahi bana son matata tana yawo. Na ce, akwai dalilina, ka ga Kwanan nan zamu zama mu biyu a Kasan ka, duk wata bukata da zan nema a wurinka dole ne ka yi mana mu biyu, inko inada nawa zan yi bukata ta ba tare da na takuraba. Ya ce, wannan

bai kai dalilin da zan bar ki ba sai dai in bar ki sbd tun farko na amsa cewa nayi miki alfarmar da kika nema,da dai tun farko na san wannance alfarmar da bazan yardaba, sai dai kimarki ta wuce in amince, sannan in dawo in ce a'a, kije kiyi koyarwa ki, amma ki tsare mutuncinki da nawa.Na sauke ajiyar zuciya 'nagode mijina, Allah ya saka da Alheri. Ya lumshe ido sannan ya bude. Yanzu wane suna za'a sa masa?
Na ce, a'a wannan shawarar tsakaninkane da Mujidat, da safe ka sameta ku tattauna. Bai ce kalaba sai ya kwanta rigingine.
Da safe falo ya zauna yace in kirata,ta fito tana yatsina cikin Riga da wnd ta zauna, ya ce, wane suna kika zaba? Ni kam mikewanayi. Ya ce,zo mana My choice. Na ce, ina zuwa. Dakina nashiga na bar su dan zancen na su ne.Ta mike daga Inda take ta koma kujerar da Ke daf da shi ta ce,Sweety kaine zaka bashi suna in dai nice nafi son sunanka don yaron yafi kama da kai. Darling kabiyani dakabani mai kama da kai. Ya waiwayo ya daga mata hannu, tsaya!baki dacikakken hankali ko? Ni ne nake bada haihuwa?Ki sawa yaron ki duk sunan da kike so amma ban da nawa kin gane ko? Ta ce, to ina son a samun Abdul-kareem. Ya ce, ya yi Allah yaraya shi.tace ameen. Sai maganar auranmu. Ya mike tace, na zata tun ranar dana haihu zamuyi maganar shine yanzu na kawo maganar za ka tashi? To bari kaji daurin auren nan in ya wuce gobe za ka ji mamakin abinda zai faru.Ya shigo daki, ina jiyo duk yadda sukayi nace, Yaya ka amince nima ina son a daura a wuce gurin kawai,ya ce, ba zanyi yanda takeso ba, tana ganin itafa wata cikakkiyar marakunyace. Bata San cewa ina daga mata kafa bane sabida Ke,nace, dan Allah kai dai gara a yi ko a wuce gurin. Sam ban zaci za a yi wani suna ba, don haka ban tanadi wani batun sunaba, kuma da zai tafi yace Usman zai kawo rago shi ma bai yi min batun suna ba, amma muna da kayan abinci na ce masa ya siyo mata sababbin kayan sawa ita maijegon,yace bazai siyoba, ko dan kyalle.

Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com Kokuma ku kasance taredamu a facebook https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Washegari tin misalin 8 na safe naji bugun gida, dama na rufo kofar gidan ina sauri zan kai yara makaranta don munyi latti, kafin in bude sai ga Mujidat ta fito da gudu tana cewa, oyoyo Momy! Kaucewa nayi ta bude, ashe 'yan uwanta ne daga Lagos su 4, Mamanta,Babanta, Kawarta da Kanwarta suka kalleni nima na kallesu, don hauka har uban suka shige cikin gidan, nasa yarana a mota na fice cike da takaicin da ya Aliyu ya ja mana. Har na dawo raina a bace. Mujidat nasamu a kicin tana ta fasa kwai ita da kanwarta suna hada abincin karyawa, ban kula su ba, na shige dakina cike da bakin ciki. Ko da naji bugun gida ban fito ba a zatona wadansu dangin nasune, amma sai na ji wayata tana ruri na daga ashe Usman ne yace Madam ki bude gida ga Ragonnan,nabude ya shigo da Ragon muka gaisa yace kuyi hakuri banzo barkaba, wallahi Sadiya takaici ne ya yi min yawa bana son ko ganin matar nan, bare Dan, sanann ga kunyarki. Nayi murmushi tare da cewa, Haba dai, gurina bakomai ya Usman. Aunty Abida fa? Ya ce, suna lafiya,naji tana cewa zatazo anjima. Na ce, yauwa Dan Allah Yaya ina jiranta yanzu, bari in kira maijegon ka ba ta, dama danginta sun zo. Ya ce, daga ina, oho bansan garinsu ba. Nace dashi. Na leka dakin sunyi dirshan a kasa suna tacin abinci suna zuba yare har da uban, a raina na ce tabdijan! Hauka. Na ce Mujidat kizo inji Yaya Usman. Ta ce, in yazo ganin yarone ya shigo mana, ni bazan fitoba. Na ce, Rago ya kawo muku, shima sauri yakeyi. Ta mike tana yatsina ta fito. Ni kam ban koma gurin su ba sai da na ji yana kirana. Madam na tafi.,na fito nace to Yaya mungode, amma lallai ina jiran Aunty, yayi dariya zan fada mata kiyi ta hkr Kinji? Na ce ba komai. Sati 1 Kawai da suka yi a gidan naga takaici,

gulma gurinsu ga shegiyar kazanta. Babanta wai ya so ya ga Aliyu saboda a yi daurin aure su zasu tafi ,kuma ganinsa baza su iya dawowa ba, shi kuma yaya yace dansu Bazai bar aikinshiba sai dai na lallabasu da cewa su tafi in Ya zo sai a je can garin. Haka kuwa sai tafiya suka yi, ya so ma har Mujidat ta bisu can, amma da yake ta san shi in har ta sa kafarta tabisu to sam ba zai nemeta ba, don haka tace aifa sam ina nan na baka lkc ka gama zaman ka dawo muyi aure.
Yafi wata sannan ya dawo, lokacin Abdul-Hakeem yayi wayo sai gogewa yake yi, don ma ba ta san bashi nono sai madara, wai bata san nononta ya lalace, na ce Allah Sarki wata rana ma ke kanki sai kin lalace bare wani nononki. Aliyu kam tuburewa yayi cewa ba zai auri mujidat ba, nima na tubure cewa ban yardaba, matsalar da ta janyo rigima har sai da Usman yazo gidan.Usman ya cewa Aliyu, alkawari Kayi tun farko, kuma musulmi ne kai ka san muhimmancin alkawari, sannan matarka tana da gaskiya ba za ku rabu ba. Mujidat da Ke daki tana jiyo wa kuwa ta fito,ta ce, ai mutuwa ce Kawai zata raba su, kuma ta dibarwa kanta lokaci in har ya cika bai ce komai a kan auran su ba za ta maka shi a kotu, sanan zata nemi yan jaridu manema labarai ta ce shine a matsayin wanda yayi mata wayo yayi mata ciki bisa alkawarin zaiaureta, amma yanzu yaki cikawa.Take Aliyu ya tashi ya watsa mata mari, sannan yace bazai auretaba, taje tayi duk abinda take ganin zai fitar da ita,da kyar Usman ya tausheshi, ni kam daki na shige ina kukan takaici mijina wanda nake girmamashi da daraja shi, amma ga wata banza datti tana wulakantashi,a fili na ce shi ya jawa kanshi.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com Kokuma ku kasance taredamu a facebook https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Sun yanke za'a kai sadakin ta can lagos, amma tare zasu har da ita da Usman da kuma su Yaya

Suleiman. Aliyu ya ce amma sai dai ta fadawa dangin ta kada suyi maganar jariri, duk ina daki ina jiyo su,lokacin ne na soma sabon kuka saboda kishin mijina ta dai tabbata lallai mijina auran zai yi.
Ya same ni a daki bayan tafiyar Usman cikinn halin kuka, ya tsorata mutuka, ya dagoni yana tanbayata dalili, ce masa na yi kaina ne kurum ke mini wani irin ciwo.ya kawo min magani ya bani a baki, sannan ya kwantar da ni.
Cikin dare na farka naganshi zaune, na dafa shi,lafiya Yaya?
Ya ce, Sadiya, ina ganin har in mutu ba zan daina nadamar laifin da na aikataba, ina cikin dana sanin zinar da na aikata da banyi ba da ban fada cikin wannan halin ba, yanzu tunanina da wane yare zan fahimtar da Iya cewar zan auri wannan yarinyar? Tsoron tunkararta nake da zancen Aunty wallahi,ban san me yasa a duk lokacin da mijina ya shiga damuwa hankalina kan tashi tausayinsa ya cikani,gaskiya da mutane suke cewa In kana son mutum kana tausayinsa. Sai na kwantar da kaina a kirjinsa, sannan nace. Don wannan Yaya Kar Ka damu, in Allah ya kaimu da safe zan samu Iya, ko kuma muje tare da kai. Ya ce, Sadiya bana son yadda nake ta saki karya don ki fitr da ni. Na ce, Allah zai dubani ya yafe min karyar insha Allah, tunda dan gyara nayi ba don batawaba,Ya rungumeni yana fadin, Sadiya Ke ce rayuwata, Ke ce abar alfaharina. Na ce, nima kaine rayuwata. Muka kwanta cike da damuwa a zukatanmu.
Goma tagota muka fito zuwa gidan Iya. Yayaya yi mutukar kyau cikin shadda waganbari mai kalar sararin samaniya(sky blue), Hula mu hadu a banki,itama kalar kayan, wanda kyan shi ya tona tsadar shi, yana ta kamshi. Ni kuwa Atamfa na sha Purple mai ratsin fari, Takalmi da Hijabina kuma farare, muka jero tamkar sabon aure muka nufi gidan Iya.
Tana zaune kan sallaya ta idar da salar walaha da fara'ar ta dubemu tana cewa. Masha Allah ina zaku haka tabarakallah amma kunyi kyau. Muka

sa 'yar dariyar yake dan nayi Imani yadda nake tsananin fargaba, hakan nanma Yaya yake ciki. Nace gurinki muka zo. Yaya ya ce daga nan za mu je kasuwane ne sai muji ko kina son wani abun?. Ta ce, bana bukatar komai Gadanga. Duk wani abu da zan nema ka ajiye min, ga firji da ka sai min ina ta saida ruwan sanyi ina samun na batarwa, ba abunda nake bukata Allah ya shi muku albarka yasa yayanku su goyaku.Muka ce ameen,tace, yan uwnka sun zo sun fada min cewa ka kai musu kayan abinci su duka ko?yayi yar' dariya, 'Iya wannan aikin Sadiya ne, ta ce duk wata in dinga sai musu kayan abinci shi ne muka fara da wannan watan. Iya ta kalle ni da dariya, 'Hali Dubu rubutun dutse, halinki dubu duk na alkhairi, na san sai ke 'yata. 'Ta kalli Aliyu. Dadin auran mace tagari kenan zata dinga bai wa mijinta shawara ta gari. Aliyu ya dube ni, sannan ya kalli Iya, 'Wannan gaskiyane Iya. Nace, 'Yanzun ma gurin ki muka zo kan wani batu.....tace, to, ya aka yi? Na kalli Yaya, shi ma ya kalle ni na ce, 'Ka fada mata. Ya ce, 'A'a ban san ta inda zan fara ba ki fada mata kawai in ta amince shi kenan. Iya ta ce, 'Ku fada min mana, kun daga min hankali. Na sunkuyar da kai, 'Iya dama mun yi shawara da Yaya ne a kan cewa zai ....za ya... 'Sai na yi shiru. Ta ce, 'Inajin ki. Na ce, 'Zai auri bakuwar nan ta gidanmu sabida tana da hankali kuma.....' Da tsawa ta katse ni, 'Ke! Da kata kin san me ki ke fada kuwa? Waye zai auri wa?
Na kalle ta 'In..
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com Kokuma ku kasance taredamu a facebook https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Yaya ne (Na nuna shi) zai auri Mujidat, tana da hankali Iya sosai. To ya ce yana son kara aure shi ne na ce ya aure ta. Iya ta rabka salati,sannan ta ce, 'Amma ban taba sanin ke mahaukaciya ba ce sai yau, ni ban taba jin inda aka ce ga wata mace

ta ce mijinta ya yi mata kishiya? Ta sake zabga salati tare da riqe haba tana kallona. 'Ko ni nan da nake tsohuwa bakeba a ce babanku zai dawo duniya zan amince ya yi min kishiya? Dan haka ban yarda ba. Muka kalli juna da Yaya, ta ce, 'Meye matsalar ka da har kake son kara aure? Ko har yanzu bata son haihuwar ne? Ya ce, 'A'a wallahi bata da laipin komai kuma ba inda ta kasa, dama sabida raya sunnah ne kamar yanda yake cikin musulunci, yarinyar nan kuma Iya ta musulunta ne in ta auri wanda ba na kwarai ba za ta dauka haka halin musulmi yake, amma mu za mu yi mata mu'amula ta kwarai yanda ba za ta yi da ta sanin musulunci ba. Iya ta ce, Eh, ai dama ke Sadiya ba a yada ke gurin magana,ni fa dan ke nake fadan nan amma ke na lura kamar zuga ki nake, wai ke ba kya kishin mijinki ne?nayi 'yar dariyar yake, sannan na ce 'Ina kishinsa mana amma hakan ba zai hana shi ya kara aure ba. Ta yi shiru tana kallon mu can ta ce, 'Ni fa ban yarda da yarinyarba, kallonta nake kamar wata 'yar bariki ko wadda ta buga duniya. Muka kalli juna,Ya ce, 'Ai kin san zaman Lagos, sannan ba ta dade da Musulunta ba.Nace, 'Eh, ba ruwan ta Iya. Ta ce, 'Oho! In ma da ruwanta ke ki ka sani tunda kin ji kin gani ai shi kenan, ni me zan ce, Allah yasa alheri. Yauwa, kwanaki yayanku kece min 'yan uwanta sun zo na ce shi ne don rashin mutunci ai sazo su min godiya. Muka sake kallon juna ni da Yaya, na ce, 'Af wannan laifina ne Iya ni ce ya kamata in rako su kiyi hakuri. Ta rike baki tare da cewa, 'Uhum! Abind ya same ki kar Allah yasa ya samu sauran dangi. 'Na ce Iya na gode bari mu tafi. Haka muka bar Iya baki bude tana mamakina,ni kuma na ce masa mu tafin dan kar ta canza ra'ayi,duk da ta amince, amma ba wai ina murna ba, bani da yanda zanyi da ya wuce in kauda da kai a yi auran, na san mata da yawa za su ga baike na amma ina san su sani DA KISHIYAR WAJE GARA TA GIDA.Daga nan gidansu Anty Abida ya ce mu tafi,,ni dai muna tafe ne ba kamar yandamuka taho dazu ba, ba wata hira bare annuri. Mun samu Usman

a gida don haka muna shiga suka fita. Aliyu ya kalli Usman 'Aboki, Iya fa ta yarda da batun Mujidat. Cikin mamaki Usman ya kalle shi tare d fadin, 'Kai haba? Aliyu ya ce, 'Allah da gaske. Usman ya ce, 'Banzata ba, ya aka yi ta amince da sauri haka? Ya ce, Kai bari kawai,yarinyar nan Sadiya aboki ba ni d abind zan biya ta, ita ce ta shawo min kan Iya har ta amince da batun,sai na lura da akwai wasu shakku daga zuciyarta, Allah yasa ba ta gane cikina Mujidat ta haifa ba.Usman ya ce, 'Ka kara rike matarka da kyau,ina fada maka a wannan zamanin ba za ka samu tamkar ta ba, ina fada maka ko Abida matata ba za ta yi wannan jan aikin ba, tana fada min sai dai ta ce tana karfafawa Sadiyane dan tasan za ta iya kuma hakanne mafita. Aliyu ya ce, Allah ya ba ni ikon riqe ta da gaskiya. Usman ya ce, Ameen, yanzun mu tafi gidan su Yaya Sulaiman mu ji yanda za a yi. Aliyu ya ce to, Allah ya rufa asiri. Abida ta dube ni ina kuka, kallo na kawai take yi bata hana ni ba kuma bata bani hakuri ba. Sai da nayi mai isa ta. Sanan na share hawaye na, sanan ta dafa kafada ta. Sadiya kada kiga cewa ban baki hakuri na barki ne ki rage radadin dake zuciyarki, gaskiya ne in ka zubar da hawaye yana rage bakin ciki, amma in tambaye ki mana? Na kalle ta da jajayen idanuna, ta ce kukan nan na menene kike yi? Murya ta a dishe tana rawa na ce, anty... Abida ina da matukar kishin Yaya Aliyu,Dan ban san irin son da nake yi mashi ba, kukaba yakunshi abubuwa dadama, amma kishin mijina shine a gaba, wai mijina zamu raba da wata, inna tuna haka hanjina na kaduwa, da na sani ban amince ya aure taba.... Sabon kuka ya kubuce mun.Tace kijure, Allah yasan nufinki, karki bari yaga karaya daga gareki, domin ba mijinkiba har mijina ya ce kin burge shi kullum cikin yabonki yake tare daba mijinki shawarar cewa yayi maki kyakkyawar ruko, dan haka ki cigaba da dannewa. Na ce, to anty zan kula, yanzu na sha kanshi ya amince in nemi koyarwa, sai dai ban san ta ina zan fara ba. Ta ce kada ki damu shugabar makarantar firamare ta L.E.A

unguwar Mu'azu kawar yaya ta ce zanyi mata magana sanan karamar hukumar Kaduna ta kudu ma babban wan su Usman yana gurin ne kuma nasan zai tai maka. Na ce, to, aikuwa nagode Anty Abida Allah yabar kauna. Tace amin. Haba ai ba komai wallahi. Nan muka wuni nakasa cin komai, Anty Abida har Dan wake tayi min wai taga inaso, amma da kyar naci uku ina taunawa tamkar ina tauna magani, ko ruwa na sha sai inga tamkar magani . Anty kanta ta shiga damuwa tana min fadan kan in kashe kai na a banxa. Na ce mata. Anty kiyi hakuri cikin kwanakin nan ko gida na bana iya cin abinci in na dauki littafin marubutan nan in dan duba sai komai ya tsaya min inkasa fahimtar me nake karantawa mai makon in karanta litafi sai dai shi littafin ya dinga neman karantani da ko ina da yar matsala inna karanta sai ya dan rinka debe min kewa. Ta ce ai duk ki ajiye batun littafi kirumgumi mai kankat wato, ALKUR'ANIR KAREEM. Na sauke ajiyar zuciya,, tabbas Anty Alkur'ani yana sanyaya zuciya mu kan musalmi bamu da kaico sai godiya ga ubangijin da yayo mu a musulmi. Ta ce haka ne Allah kasa mu mutu a cikin musulumci muna a musulmai. Na ce amin.

Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Kafin su dawo ta sani na wanke fuskata nayi yar kwalliya, duk da fara'ar da nadingayi sai da yaya ya gane nayi kuka, duk lokacinda na kalle shi sai in ga idanunsa na kan fuskata har dai ya kare ya ce Sadiya kukan me kikeyi? Muka kalli juna da Anty abida ta ce, sam bata yi kuka ba me kagani? Yayi dan yake shi dole murmushi, ko ba jami'in tsaro bane ni, kun san daini ba yaro bane. Na share zan cen da cewa, yaya mu tashi dan yara na jira na in daukosu. Ya ce madan saurareni. Abida ta kalle shi ya ce, nifa bana son abin da

zata shiga matsala, in auren nan zai kawo mata damuwa wallahi sai a fasa duk abin da zai faru ya dade bai faruba kowa ya ji cewa nayi wa wata ciki ta haihu, daga nan fa? Na runtse ido, don Allah yaya mu bar maganan nan, nace maka ba damuwa nake ciki ba, ka yarda dani. Usman ya ce aboki ina ga dai na dawowa da hannun agogo baya din nan a bar shi. Abida ta ce ai sadiya jaruma ce bata cikin wata damuwa, kuma malamai sun sha fada muna cawa in Allah ya rufa maka asiri yayin da ka aikata wani laifi to kai kada kayi kokarin tonawa kan ka don haka barin batuna haka shine mafi a a'ala. Haka dai muka baro gidan nasu bayan sun yi mana rakiya.
Saty daya bayan nan suka shirya tafiya lagos, sai dai ban da ya Sulaiman saboda suna son yan da haduwar su da dangin mujidat zai kasan ce, haka nan basa son yanda ya Sulaiman ya san cewa dan da ta haifa na shi ne. Sun tafi da Usman da shi Aliyun da kuma Mujidat da Danta. Sai dai lissafin da aka yi masa ya same wuce hankali, domin ko auren Sadiya bai kashe wannan kudin ba, sannan kudin sa da ke accout yayi shirin siyan wani gida ne da aka yi masa tallansa can kasan su a sabuwar unguwa da ke nan unguwar Mu'azun. Ya kalli Usman ya ce aboki ni fa ba zan iya biyan wayan nan kudinba. Usman ya ce, to ka kirata ta fada musu baza ka iya yin al'ada ba. Ya kalli waliyin ya ce a kirata. Sai suka ce ai su al'adar su ba a magana da amarya sai su waliyanta. Usman ya ce to su basa yin wanan al'adar sadaki kawai zasu biya. Sauran suka ce sam ai tunda ta haihu a tasu al'adar yin biki dolene, kuma abubuwan al'ada dole ne, domin ita mai albarka ce mai haihuwa ce, sannan ba dama ya ce ya fasa tunda ta haihu.
Shi da Usman suka kalli juna a ran shi ya ce lallai ya debowa kanshi ruwan dafa kanshi. Usman ya ce kawai ka basu inya so sai ka sai fili bana son a samu matsala. Nan dai ba da son ran shi ba ya amince bayan sun fita suka tafi banki in da ya ciro kudi suka dinga yi masa lissafi yana ba su, nan fa suka ce jibi za su yi hutu, suka amince a

haka. Ni kam ko da suka dawo bai fada min ba gurin Anty Abida na samu labarid Usman ke fada mata, na ce shi dai ya sani can da yawarsa. Idanu na zuba ina kallonsa yau da na ga yanzun yana dan zakewa tare da rawar kai, sam ban zata ba, ya sa a yi gyaran gida. An yi fenti na kwashe kayan yarana daga dakin da ta zauna tunda nan za'a sa ta, ya ce da ya so canza min gado,amma in yi hakuri ko daga baya ne. Yaba ni dubu talatin,na yara ashirin na karba na aje tare da cewa mun gode. Na dauki waya ta ina dannawa ya ce, Wai Sadiya akwai wani laifi da nayi makine?na kalleshi' Me ka gani? Ya ce, Na ga tun jiya da na zo ba wata fuska a gurinki?Na maida kaina ga kallon wayata,sannan na ce, Akwai abin da ban makaba daga cikin wanda na saba yimaka?Yace, A'a,kin min komai MY CHOICE, sai dai ni na gane kamar ba ki da walwala. Na ce, Ba ka yi min komai ba. Ya ce, To anjima zan tafi, Na ce, Allah ya kai mu. Har ya kai bakin kofa na ce, Au! Na manta in fada maka an dauke ni amma ba aprimary ta nan unguqar Ma'azu ba, ta can Tudun wada. Ya tsaya yana kallona, nima shi nake kallo don son jin ta bakin shi,a zuciyata ina cewa yanzun dai a ce ya hana ni, tabdijan! Da sai ya ji magana. Tamkar ya sani sai ya ce na san kina zaton zan hana kineko? Ai ba ni da yanda zan yi tunda na rigana yi miki alkawari,amma ki sani raina baya so. Ban ce kala ba na ci gaba da danna wayata shi kuma ya fita.
Ban tabbatar da cewa ina da kishi ba sai da lokacin auran ya gabato,wallahi ko abinci kasa ci nayi duk datausar da Aisha ke min da kuma Anty Abida dan ganin na kwantar da hankalina, amma na kasa, bana bacci sosai duk da cewa bana nunawa Yaya damuwata sai dai shi duk lokacin da muka yi waya sai ya yi min korafin in daina damuwa in kwantar da hankali,To kurum nake ce masa, amma zahirin gaskiya zantukansa ma soya min rai suke yi.
Ana gobe daurin aure zasu tafi can Lagos din ina kallo shi yana ta shige da fice yana shiri,an zuba sababbin dinkuna an sai Huluna da Takalma sai

ina mamakin mutumin da na dinga shan kan shi da kyar shi ne yake zumudi. A fili na ce Allah yasa abin ya tsaya nan. Ya fito cikin shiri ina kwance kan gadon yara ya ce 'My Choice mun shirya,na dago na kalle shi, yayi matuqar kyau cikin Shadda Wagambari Blue shar kaladaya da hularsa mu hadu a banki, kamshinsa ya cika gidan, kishi ya kama ni mai tsanani,na kau da kai gefe. Ya ce, 'My choice yaya ne? Ban tanka masa ba sai zuciyata ta ce gwada shi ki gani da yake cewa in na ce ya fasa zai fasa,in ya so duk ma abin da zai faru to ya faru. Ya tallabo fuskata. 'My Choice, yaya ne? Na ce, 'Ni fa gsky na sake tunani a kan wannan auran, gaskiay ina tsoron abin da zai biyo baya. Zai fi kyau a barshi. Zumbur ya mike tsaye daga russunawar da ya yi, na kalle shi ga mamakina fuskarshi daure, ya ce, 'Me ki ke nufin maidani? Karamin mutum? Kin sa mun yi magana yanzun kuma kizo ki ce ke kina jin tsoro, ya kamata ki fadi haka ne tun kafin yau, sai dai ki yi hakuri,mamakida tsoro suka sa na kasa daina kallonsa sannnan ga hawaye yana ta zuba tamkar an bude famfo, na girgiza kai tare da sauke ajiyar zuciya,sai kuma ya zauna kusa da ni tare da dafa kafadata. My choice bana nufin cutar da ke kece kika karfafani kika nuna min yin auran nan shine mafita, to me zai sa yanzun ki bijiro min da wani sabon batu bayan aski ya zo gaban goshi? Kuka ya kwace min na shiga rera shi, tsam ya makaleni jikinsa yana lallashina. Sadiya in kin ce baki so wallahi abar shi. Ya ciro wayar shi yasoma dannawa. Bari na fadawa Usman ya kira Yaya Sulaiman ya fada masa cewa nafasa.ina jiyo shigar wayar ta soma ringing a can,da sauri na dago na amshi wayar da sauri na katse. Ya ce, yaya kuma za ki katseki bani in dakatar dasu su daina shiri. Na cecikin shagwabar kuka, Ni fa ban ce ka fasa ba.yasa hannunsa ya dago fuskata,To me kika ce?Na kalli cikin idon shi 'In ka aure ta zaka daina sona? Sai kurum naji bakin shi cikin nawa, minti1muka dauka, sai wayarshi ta shiga ruri,ya sakeni tare da daukar Wayar. Usman ina zuwa. Ya katse ya

kalleni. My Choice in na yi rantsuwa bazan yi kaffaraba Ke ce 1 tak nake so, kum na soma son ki ne tun Ikcn da kika soma zama mace. Da farko ban fahimci ina sonki bane sai da Usman ya kwadaita mini da nazo iya ta ki sai na samu kaina da kasa hakura, wannan ya tabbatar min cewa ina mutukar sonki,Ke ce zabina, kada ki damu da Mujidat sam ba na son ki hada son ta da naki, Ke ba ita ba in miki ta mahaukaci duk duniya ba wata mace da nake so ko kuma zan sota sama da ke, ki rike wannan a cikin zuciyarki,so 1 tak Ke na ke yiwa shi.,lumshe ido na yi inma karya Yayaya fada min to na yarda don gaskiya maza da ace zasu gane furta son ka ga matar ka komai dadewar aurenku yana susutar da mace komai shekarunta ta ji ta tamkar sabuwa,amma matsalar maza musamman irin na yankinmu ba sa iya cewa matar su suna sonta, ko wasu kalamai na soyayya irin wanda suke yi mata yayin yakin neman aurenta da zarar sunga cewa sun aurenta shi Kenan ta tsufa Nima haka na ji tamkar farkon aurenmu duk damuwar dake cikin zuciyata sai ta gushe, sabida ina son a so ni,ina son a nuna min soyayya, ina son a fada min kalaman so. Nasa hannu a kumatun shi na shafa ina kallon cikin idon shi, Yaya na gamsu da kalamanka, Allah ya tsare hanya gobe zaku dawo? Ya ce, insha Allah ko jibi, tunda da nisa in mun taso da yamma ko da dare sai safe zamu iso. Na ce shi Kenan. Ya mike tsaye, me zan sayo miki a can? Na ce, gdnsu lesuka, in ka siya min zanyi murna. Ya ce insha Allah zan zabo miki masu kyau. Na ce to nagode. Har waje na raka shi. Sai dai duk da haka kasa bacci nayi daren ranar sai damuwa da sake saken zuci.

Washe gari kuwa data kasance ranar daurin aure ba zan iya lissafa tashin hanklin da na shiga ba. Da safe kasa zama na yi a gidan na tafi gidan Iya wai don in manta da batun auren amma duk da haka na kasa sukuni, har Iya ta fahimta, sai kurum naji ta ce. Sadiya, hakika kishi wani abu ne mai rai, amma yana da sauki in kin saukakashi, ina son ki nutsu ki rike girmanki. Shawarar da zan

baki ki kara zage damtse gurin kyautatawa mijinki kada ki dauki halayen wasu matan masu cewa in miji ya kara aure zasu daina yi masa komai suce ya je can matar da ya auro tayi masa, wannan kuskure ne, don in aka samu wadda ta san hannunta kafin ki samo mijinki sai wani ikon Allah,ki zama a gidanki Ke ce uwar kowa. Ina nufin duk abinda ya taso na kudi ko matsalar lalacewar wani abu a gida Kar ki tsaya jiransa kiyi da kudinki in yaso in yazo kya karba ko yaturo miki, sannan ba'a fata in har sabani ya shiga tsakaninki da ita tunda an ce zo mu zauna zo mu saba, to kada ki sake ki fara kai kara Kinji ko? Na ce, to. Yauwwa sabida in kinyi nazari cikin ya'yanki mai yawan kawo kara duk gaskiyarshi sai kinji haushinsa. Na ce, haka ne. To ki rike hakuri da addu'a ki dinga yawaita karatun Alkur'ani mai girma, ki zauna da ita zuciya1, sannan ga aikin ki ma, ai ni naji dadin barin ki da yayi wannan koyarwar, na ce, nima naji dadi iya, don ina da yara gara dai yanzu da muke mu 2 aikin ya dauke masa matsalolina in ina samu ba sai na jira shi ba, kudin da ya bani ma nawa da yara wai muyi siyayya su dai na Dan sai musu wani abu, so nake in hada jari in dinga saye da siyarwa. Iya tayi dariya tare da cewa, da kyau Sadiyayyena. Haka nayini Iya tana kwantar min da hankali tare da bani shawarwari sai kusan 10 na dare na debi ya'yana ta raka mu har gida, nima na sake rako ta hanya.ina sa hakarkarina a kan gado na dauko wayata nakunna dama yinin ranar kashe ta na yi. Nan fa sakonni suka soma shigowa na yaya sai na Aisha da Anty Abida, na su na soma dubawa. Tanbayata suke ina naje sun zo ba nanan? Na yi dan murmushi, a fili na ce da kun zo gidan Iya ni kam ba zan yi wani taro ba, sai na soma duba nashi,duk kusan yana nuna damuwane akan ya kira bai sameni ba. Sai na karshe da yake cewa sun taso 9 suna hanya, akwai yiwuwar su iso kafin 9 na safe, kuma suna tare da wasu daga danginta dan Allah ta tanadar musu abinci. Kiran Abida ya katse karatun sakon da na keyi, na daga muka gaisa, ta ce min, ina na shige yau? Na ce

ina gidan Iya,tace to, ki yi sammakon tashi don mijinki zasuyi shigowar safe ne, nace Anty me zanyimusu?tace karin kumallo mana kiyi zuciya1 kada ki sa kishi ciki, bakin kine, kin kuma san darajar baki a musulunci. Na ce to Aunty zanyi. Tin 4 na tashi na fara firar dankali da nayi sallah kuma na hau suya, har kaji biyu nayi musu farfesu, kwai ma isasshena yi musu kwai da kwai na dafa ruwan tea mai yawa, sannan na gyara gidana nayi wa yara wanka na zabo musu sababbin kaya nima na sheka nawa adon.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com Kokuma ku kasance taredamu a facebook https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Takwas daida na ji tsayawar motoci,gabana ya yanke ya yi wata muguwar faduwa,sai na hau karanta Hasbunallahu wa ni'imal wakil. Na mike na je na bude musu kofa gabana yana ta faduwa,zuciyata tana maimaita addu'a.suka shigo suna yi min sannu, wasun su suna kallona wani iri,amma duk da haka na saki raina ina yi musu sannu da harshen Turanci.Najee na bude musu dakin suka yi sororo a tsakar daki don ga al'adarsu miji ke shiryawa mace daki ya zuba komai, ita kuma iyayenta su yi mata kayan sawa, nan fa suka soma yare, duk da bana ji amma ganin yanda suke magana suna tabe baki na fahimci zancen nasu bana dadi ba ne, naje nasoma fito musu d kuloli. Sai gasu Yaya sun shigo, na kirkiro fara'a ina yi musu sannu da zuwa. Falo suka je suka zauna na gabatar musu suma da abin kari, na kula yaya ya ji dadin yanda na saki jikina na kuma yi musu abin kari.Nan nabarsu nayi daki,bayan Mujidat da danginta sun gama karyawa sai suka samu su Aliyu da Usman suna yi musu korafin ba su ga kmai a dakin ba.Usman ya ce, Mu a nan da kaya amarya take zuwa. Suka ce su kam ba haka ba ne, nan suka fito masa da akwatunan amarya har da na mijin da na Maman shi da kuma na

danginsa. Aliyu ya ce shi kenan zai siya daga baya, amma yanzun a kwaso na dakinsa a sa mata,sukace bakomai. Ina dakin nashi ya shigo wanda zuwa yanzun ya zama nawa,ya zauna. Sadiya kin ji wata sabuwa. Na kalle shi, ya ce, Wai ni zan sai mata gado. Na ce, ina zaton haka al'adar su take don mun taba yin zancen da wata 'yar ajinmu da muka yi N.C.E take ba mu labarin al'adunsu, miji ke yin kayan daki kuma sadakin su yana da tsada, amma mace za ta ja jari da su ita ce za ta rike gida,wasu kuma jarin daban miji zaibada, wadanda ba Musulmi ba sun fiyi, Musulminsu kamsai sunyi aure suke tarewa gidan mazajensu,yace,nidai yanzun ya za'a yi? Na ce su zo su dauki wannan gadon. Na tsura masa ido cikin mamaki,sai ya ce, ko ya ki ka gani? Na mike na nufi dakina bayan na ce, Me zan ce kai da abinka. Na shiga dakina na soma kallon dakin ina lissafa yanda zan gyara shi ni da yarana da na bar musu gadona tunda dama katifu gare su. Sai ga shi ya shigo.Haba Sadiya,me zai sa ki yankemin wannan hukuncin? Nazo miki da shawara amma sai ki yi watsi da ni kitaho abin ki? Na ce, Yaya kainefa da abinka kuma ka ba matarka, mene ne laifina dan na taho? Yace, Ok, kije amma ki sani kada nan gaba ki ce na daina kawo miki Shawara,kin sani dai ke ce kurum nake tunkara da duk matsala ta. Shiru na yi dan nasan in hakan ta faru lallai ba zan zama uwar gidaba. Ya mike zai fita na ce, Yaya" ya dawo,Mene ne? Na ce, Shi kenan ka yi hakuri. Ya zauna tare da kamo hannuna, Nagode da ki ka fahimce ni, yanzun ya ki ke ganin za'ayi? Na ce, Ka ba ta,ni kawai sai naringa kwana a nan da yarana. Ya tsura min ido, To nifa? Na ce, Ba komai ka yi ta kwana dakinta. Ya yi dan murmushi, Har yanzun baki huce ba.Na yi 'yar dariyar yake, Bana fushi da kai. Yace, Zan siyo katifu yau a sa can dakin in komai ya warware zan canza gadajen gidan.Na ce to maimakon ka ba ta tsohon gadon ba gara ka sai mata katifar ba? Amma yanda ka gani, Ya ce na riga na fada musu ne na ce to su dauka bari. In zo in kwashe kayan na wardrobe din. Ya ce,

A'a, gado kawai da katifa za ta dauka. Na ce, Shi kenan, Allah ya rufa asiri. Ashe tashin hankali yana gaba,sai lokacin bacci, Mujidat ta kira shi a waya wai tana jin bacci, ya kalle ni muna zaune kan gado,sannan yaci gaba da magana. To ki kwanta mana. Ta ce, Ba dakin ka zan kwana ba? Ya ce, A'a yanzun bani da daki in danginki sun tafi na kwana adakinki. Mamaki da haushi suka cika ni, ga kishi kamar in hade raina, na ce, Kuje dakin naka mana? Yaja tsaki tare da cewa, Don Allah ki bar wannan maganar. Na kwanta tare da juya bayana na rungume yarana bankara sauraron shi ba, shi ma ya kwanta a daya gefen
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Washe gari tun Asbahi suka soma shiri,suna karyawa suka tafi, wata daya ce daga cikinsu kadai ta yi min sallama da godiya, suna kama ina zaton yarta ce dake illorin din, domin nayi dawainiya dasu sosai ta fannin abinci. Ya tsaya da su sun shiga gurin Iya sun gaisa duk da cewa ba sa jin yaren juna, sannan ya wuce dasu zuwa gareji. Ranar ne matan Yaya Sulaiman da su Anty Abida sukayi ta zuwa ganin Amarya. Anty Abida ta yi ta yi min fada wai ya zan sa abu a cikin raina ga shi nan duk na rame, na ce Anty dole in sa a raina, ba za ki fahimci zafinkishi ba, duk irin bayanin da zan yi miki, kuma bana fatan a yi miki ki ji.Anty Abida tace, Ameen,don Allah ina son ki saki ranki. Amarya dai tana daki bata fito ba, da za su tafi na raka su ganin amarya ta ci rigarta da wando na bakin Jeans, danta yana cikin gadon shi ta yi ruf daciki kan gadon da suka kafa tana chatting, a yatsine ta amsa sallamar,sannan aka gaisa,suka yi fatan alkhairi suka fita.
Daran ranar ne ya hada mu a falo yana yi mana nasihar zama lafiya, sam ban san me yake cewa ba, ina can gurin tunani. Yau ga shi abin da nake karantawa cikin littattafai ya zo kaina, ji nake

tamkar cikin mafarki, ashe dai nima za a min kishiya. Girgiza nin da yayine ya sa na dawo cikin hayyacina,cikin damuwa ya ce, Menebe? Na girgiza kai ba komai. Ya ce, ina tambayar ki game da kwana,na ce, Nawa nawa? Nayi hamma kirkirarra, sannan duk yadda kace. Ya ce, To a bar shi bibbiyu kamar yanda aka fi yi. Na ce shi kenan. Ita dai tana ta jijjiga danta,na sake kirkiro hamma, zanje in kwanta bacci. Ya kalli agogon bango; Da wuri? Na ce, Na gaji ne. Na kalli amarya wadda ta sha leshi kai ya ji gashin doki ya zubo har kafada, na ce, Sai da safe,ta dube ni da 'yar yatsina eh, dama ban jira amsar ta ba na yi tafiyata. TABDI! Daran ranar kasa bacci na yi har zuga ni zuciyata ta dinga yi wai inje in labe inji me suke yi, amma sai na fi karfinta inda na yo alwala na yi ta sallah in nagaji in dauki Alkur'ani nayita karantawa,sai da na yi sallar Asubahi sannan na kwanat. Allah ya taimake ni yarana suna cikin hutun makaranta ne, don haka da na tashesu muka yi sallah sai muka koma. Ban farka basai tara, ina tashi Mama ta tashi, sai da na yimusu wanka sannan muka fito.....zandakata anan zuwa lokaci na gaba,fatan zaku kasance tare dani
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Darajar Yayana3-03
Posted by ANaM Dorayi on 12:12 AM, 04-Apr-16
Under: DARAJAR 'YA'YANA
___________________NA
___________HALIMA K/MASHI
Assalamu'alaikum,akaro na barkatai gani na dawo domin kawo muku cigaban labarinmu ,fatan kuna sane da inda muka tsaya.
Yayi shiru. Na ce Hello, kana jina? Eh, kin fadawa Iya ne? Na ce, nanmuka amshi haihuwar tare,

Kasan cewa taso ta gano cewa danka ne? Dan yaron yayi kama da kai fiye da duk yaran gidan nan.Da karfi yace Haba dai! Wlh, yaushe zaka zo? Yayi dan tsaki, gaskiya bani da ranar zuwa, zan turo miki kudi kiyi duk abinda ya dace. Nace, zuwan ka yana da muhimmanci, sabida Mujidat zata iya tana komaifa, inbata gankaba. Ya ce, to zan zo kafin suna inkuma dawo
Gurin aikina. Nace to saikazo. Na kira auntyAbida na fada mata, haka ma Aisha kawata.Makota duk suna ta shigowa Barka. Su kausar ma nasa sunje sunga baby,na fada musu cewa kaninsune, suna ta murna har da kausar. Aisha ranar datazo barka tana daukan yaron tace, kai Sadiya yaron nan yana kama da Abban kausar. Nace, haka ake ta cewa, dama kin san mutane sun ce in mai ciki tana yawan kallon mutum ta kan haifi mai kama da shi. Ta yi Yar dariyar yake,tare da cewa, hakane kawata.Mai jego kam ina kallon ta sai harara take watso mana. Muna shiga dakina tace, Sadiya anya kuwa ba kanshin gaskiya a cikin lamarin matar nan? Kin san halin mazannan ko dai Dan sa ne? Ki yi hakuri kamarce naga tayi yawa. Nace, hum! Ke dai bari kawata, tsakanina dake nasan amanace, wlh dansane ciki yayo mata, yanzun data haihu zasuyi aure. Aisha amana na fada maki ko iya bata San wannan ba. Aisha ta zabura tare da fadin, kan uba! Lallai Sadiya ban taba sanin cewa Ke sakarya bace sai yau, yayowa wata ciki sannan ki yarda ta zauna maki a gida? Wallahi da ace nasan haka ne in nazo barka shegiya nake,kin ma daure masa gindi kenan gobe ya kara.Na ce, Aisha ki fahimta, uban 'ya'yanane,mijina kuma yaya zanyi? Nawa ganin rufin asirinshi Nawa ne, kuma na yara nane. Ta yi tsaki bana Jin zan fahimceki, in tazo gidan ta koreki kin ga ai sai kiji dadin rufa masa asirin. Na ce, nasan dama bazaki fahimceniba, shi yasa tun farko ban sanar da Ke ba, dan na sanki. Ta dauki yarta tasa a baya,ta suri jakarta da hijabinta, Ni kin ga tafiyata. Na bita ina fadin, "Dan Allah Aisha ki saurareni. Ki tayi ta tafi abinta. Na ce to shi Kenan in kin huce za muyi waya ta ce ni kar

ki kira ni. Na dawo daki na kwanta kan gado ina hawaye, in na tuno Yaya zasuyi aure da Mujidat Abin na daga hankalina ya kuma sani kuka. Ranarr da suka cika kwana 5, sai ga Yayakusan 10 na dare, Ni ce ma na bude masa kofa, ya janyo ni jikinsa,ni kaina bansan me yasa jikina yayi sanyi ba kuma banyi wani farinciki da ganinsa ba. Ya dago fuskata, sannan yahaskani da wayarsa, lafiya my choice? Na sa hannu na tare hasken,lafuya mana Yaya mai ka gani? Na karbi jakar hnnunsa tare da cewa sannu da zuwa,bai amsa ba sai dai ya ce, na ganki cool ne, kamar ba kiyi farin ciki da gani na ba. Na ce, bacci na fara. Sannan nayi gaba na bude masa daki ya shiga. Ya zauna bakin gado tare da fadin, na gaji yau Sosai,8 ta wuce na baro Abuja, kuma da safe zan wuce na zone Kawai sabida kin nuna zuwan nawa yana da muhimmanci. Na ce, to Kayi wanka zaka warware. Ya ce to. Kafin ya fito wanka na kawo masa tuwo daman shi nayi a daren miyar zogole. Sai da yaci na fitar da kwanukan, sannan na shiga gurin Mujidat tana zaune da waya tana chatting, na ce, ya kamata fa ki dinga bacci. Ta ce, ba zan yi hira da kawayena ba? Na ce, kuyi tayi, akawo yaro babanshi yazo. Ta kalli yaron sannan ta kalleni, ya yi bacci. Na Isa gurin yaron na dauko shi, ban tsaya jiranta ba na kai shi. Aliyu ya mike tsaye zumbur likacin da ya kalli yaron duk yadda Sadiya Ke bashi labarin kamannin shi da dan bai zaci har hakaba. Ya kalli yaron kusan minti 1, sannan ya miko mini tmkr yana tsorace,na maida hannuwana baya. Kayi masa addu'a kamar sauran yaran ka duk dadai baka samar da shi ta hanyar da shari'a ta amince ba, sannan ka yi masa hudu ba,ya daga murya rikeshi mana Sadiya. Na juya na fita. Abin mamaki sai ga Mujidat labe tana lekenmu, na tsaya turus ina kallonta, ita ma ta yi tsuru-tsuru na ce, a'a dama kina min labe? Ta soma Sosa kai, sai kuma ta shiga borin kunya, kin zo kin daukarmin yaro ba dole inbiba? Na ce, kina zargin zan cutar miki da yaro ne? Yaya ya fito ya mika mata yaron "ungo yaron ki kar ku tada min

da yara suna bacci. Ta amshi danta ta tafi, ni kam a gurin na tsaya na ma rasa tunanin da zanyi, tun yanzu kenan kafin a daura Auren? Shi kam bai so yanda ya yi ba kada ma mu tada masa yara suna bacci, maimakon ya gargadeta kan cewa Kar tasake yi min labe, bai yi hakan ba sai ya shige abinsa. Ni kam dakin yarana na nufa amman ko zama ban yi ba sai ga kiranshi, sai da wyrta kusa tsinkewa sannan na daga. Meyene? Yace, zomana,sai da na dan bata lokaci, sannan na je. Kai kawo na samu yana yi a cikin dakin, ina shiga ya nufo ni ya kama hannuwana. Sadiya asirin da muka rufa zai tonu sabida kamannina da yaron nan ya dauko,ina ganin gara mu fadawa Iya Kawai ita kuma Mujidat ta yi tafiyarta tunda dama dan Kar Iya su sani ne zan aure ta, ni wallahi bana son ta, zata iya tarwatsa min iyali,na zame hannuna daga nasa na zauna bakin gado tare da rike kaina na ce, Yaya ba dan Kar asirin ka ya tonu Kadai ba ne na ce ka aureta, don gudun kada kuci gaba da haihuwa a titi babu aure, don nasan bazaku rabuba. Shima ya zauna, sai dai in itace baza ta rabu dani ba Sadiya, amman wallahi ni tuni na barta,na girgiza kai, Yaya yin Aurenku yafi a kan barin shi, don Mujidat ta tabbatarmin da hakan kuma na San zaku iya... hawaye suka soma zubomin cikin rawar murya na ce. kuma duk laifin kane. Ya kwanto ni jikinshi, wallahi Sadiya nayi nadama matuka, kuma naji kunyarki Sosai ki yi hakuri kidaina kuka, Kecefa kike Karfafa min gwiwa,kike bani shawara. Ya dago fuska ta. Hankalina yatashi da yawa ganin kamannin yaron nan,nasan sai dai mutane su ji mu Kawai, ammababu wanda zai yarda cewa ba yaro na bane. Ya share min hawaye. Ki yafe min. Na ce, Yaya ni dai alfarma Kawai zan roka a gurin ka guda biyu. Da sauri ya ce, na miki alkawarin yi miki su fadi inji.

Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com Kokuma ku kasance taredamu a facebook https://mbasic.facebook.com/HAUSA-

Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_
ID10%2C737012347
Na ce, na farko duk rintsi kada ka juya min baya ko ka wulakanta ni. Ya rike kafaduna muna kallon juna, insha Allahu Sadiya ba zan miki ba ko bisa kuskure insha Allahu. Nace sai na biyu, izini zaka yi min in nemi koyarwa a makaranta, ko L.E.A ta nan unguwar Mu'azu. Ya yi shiru yana nazari, can ya ce, kin gane Sadiya ba wai ina son hanaki bane, nafison ki nutsu a gida wallahi bana son matata tana yawo. Na ce, akwai dalilina, ka ga Kwanan nan zamu zama mu biyu a Kasan ka, duk wata bukata da zan nema a wurinka dole ne ka yi mana mu biyu, inko inada nawa zan yi bukata ta ba tare da na takuraba. Ya ce, wannan bai kai dalilin da zan bar ki ba sai dai in bar ki sbd tun farko na amsa cewa nayi miki alfarmar da kika nema,da dai tun farko na san wannance alfarmar da bazan yardaba, sai dai kimarki ta wuce in amince, sannan in dawo in ce a'a, kije kiyi koyarwa ki, amma ki tsare mutuncinki da nawa.Na sauke ajiyar zuciya 'nagode mijina, Allah ya saka da Alheri. Ya lumshe ido sannan ya bude. Yanzu wane suna za'a sa masa?
Na ce, a'a wannan shawarar tsakaninkane da Mujidat, da safe ka sameta ku tattauna. Bai ce kalaba sai ya kwanta rigingine.
Da safe falo ya zauna yace in kirata,ta fito tana yatsina cikin Riga da wnd ta zauna, ya ce, wane suna kika zaba? Ni kam mikewanayi. Ya ce,zo mana My choice. Na ce, ina zuwa. Dakina nashiga na bar su dan zancen na su ne.Ta mike daga Inda take ta koma kujerar da Ke daf da shi ta ce,Sweety kaine zaka bashi suna in dai nice nafi son sunanka don yaron yafi kama da kai. Darling kabiyani dakabani mai kama da kai. Ya waiwayo ya daga mata hannu, tsaya!baki dacikakken hankali ko? Ni ne nake bada haihuwa?Ki sawa yaron ki duk sunan da kike so amma ban da nawa kin gane ko? Ta ce, to ina son a samun Abdul-kareem. Ya ce, ya yi Allah yaraya shi.tace ameen. Sai maganar auranmu. Ya mike tace, na zata tun ranar dana haihu zamuyi maganar shine

yanzu na kawo maganar za ka tashi? To bari kaji daurin auren nan in ya wuce gobe za ka ji mamakin abinda zai faru.Ya shigo daki, ina jiyo duk yadda sukayi nace, Yaya ka amince nima ina son a daura a wuce gurin kawai,ya ce, ba zanyi yanda takeso ba, tana ganin itafa wata cikakkiyar marakunyace. Bata San cewa ina daga mata kafa bane sabida Ke,nace, dan Allah kai dai gara a yi ko a wuce gurin. Sam ban zaci za a yi wani suna ba, don haka ban tanadi wani batun sunaba, kuma da zai tafi yace Usman zai kawo rago shi ma bai yi min batun suna ba, amma muna da kayan abinci na ce masa ya siyo mata sababbin kayan sawa ita maijegon,yace bazai siyoba, ko dan kyalle.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com Kokuma ku kasance taredamu a facebook https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Washegari tin misalin 8 na safe naji bugun gida, dama na rufo kofar gidan ina sauri zan kai yara makaranta don munyi latti, kafin in bude sai ga Mujidat ta fito da gudu tana cewa, oyoyo Momy! Kaucewa nayi ta bude, ashe 'yan uwanta ne daga Lagos su 4, Mamanta,Babanta, Kawarta da Kanwarta suka kalleni nima na kallesu, don hauka har uban suka shige cikin gidan, nasa yarana a mota na fice cike da takaicin da ya Aliyu ya ja mana. Har na dawo raina a bace. Mujidat nasamu a kicin tana ta fasa kwai ita da kanwarta suna hada abincin karyawa, ban kula su ba, na shige dakina cike da bakin ciki. Ko da naji bugun gida ban fito ba a zatona wadansu dangin nasune, amma sai na ji wayata tana ruri na daga ashe Usman ne yace Madam ki bude gida ga Ragonnan,nabude ya shigo da Ragon muka gaisa yace kuyi hakuri banzo barkaba, wallahi Sadiya takaici ne ya yi min yawa bana son ko ganin matar nan, bare Dan, sanann ga kunyarki. Nayi murmushi tare da cewa, Haba dai, gurina bakomai ya Usman. Aunty Abida fa? Ya ce, suna

lafiya,naji tana cewa zatazo anjima. Na ce, yauwa Dan Allah Yaya ina jiranta yanzu, bari in kira maijegon ka ba ta, dama danginta sun zo. Ya ce, daga ina, oho bansan garinsu ba. Nace dashi. Na leka dakin sunyi dirshan a kasa suna tacin abinci suna zuba yare har da uban, a raina na ce tabdijan! Hauka. Na ce Mujidat kizo inji Yaya Usman. Ta ce, in yazo ganin yarone ya shigo mana, ni bazan fitoba. Na ce, Rago ya kawo muku, shima sauri yakeyi. Ta mike tana yatsina ta fito. Ni kam ban koma gurin su ba sai da na ji yana kirana. Madam na tafi.,na fito nace to Yaya mungode, amma lallai ina jiran Aunty, yayi dariya zan fada mata kiyi ta hkr Kinji? Na ce ba komai. Sati 1 Kawai da suka yi a gidan naga takaici, gulma gurinsu ga shegiyar kazanta. Babanta wai ya so ya ga Aliyu saboda a yi daurin aure su zasu tafi ,kuma ganinsa baza su iya dawowa ba, shi kuma yaya yace dansu Bazai bar aikinshiba sai dai na lallabasu da cewa su tafi in Ya zo sai a je can garin. Haka kuwa sai tafiya suka yi, ya so ma har Mujidat ta bisu can, amma da yake ta san shi in har ta sa kafarta tabisu to sam ba zai nemeta ba, don haka tace aifa sam ina nan na baka lkc ka gama zaman ka dawo muyi aure.
Yafi wata sannan ya dawo, lokacin Abdul-Hakeem yayi wayo sai gogewa yake yi, don ma ba ta san bashi nono sai madara, wai bata san nononta ya lalace, na ce Allah Sarki wata rana ma ke kanki sai kin lalace bare wani nononki. Aliyu kam tuburewa yayi cewa ba zai auri mujidat ba, nima na tubure cewa ban yardaba, matsalar da ta janyo rigima har sai da Usman yazo gidan.Usman ya cewa Aliyu, alkawari Kayi tun farko, kuma musulmi ne kai ka san muhimmancin alkawari, sannan matarka tana da gaskiya ba za ku rabu ba. Mujidat da Ke daki tana jiyo wa kuwa ta fito,ta ce, ai mutuwa ce Kawai zata raba su, kuma ta dibarwa kanta lokaci in har ya cika bai ce komai a kan auran su ba za ta maka shi a kotu, sanan zata nemi yan jaridu manema labarai ta ce shine a matsayin wanda yayi mata wayo yayi mata ciki bisa alkawarin zaiaureta, amma

yanzu yaki cikawa.Take Aliyu ya tashi ya watsa mata mari, sannan yace bazai auretaba, taje tayi duk abinda take ganin zai fitar da ita,da kyar Usman ya tausheshi, ni kam daki na shige ina kukan takaici mijina wanda nake girmamashi da daraja shi, amma ga wata banza datti tana wulakantashi,a fili na ce shi ya jawa kanshi.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Sun yanke za'a kai sadakin ta can lagos, amma tare zasu har da ita da Usman da kuma su Yaya Suleiman. Aliyu ya ce amma sai dai ta fadawa dangin ta kada suyi maganar jariri, duk ina daki ina jiyo su,lokacin ne na soma sabon kuka saboda kishin mijina ta dai tabbata lallai mijina auran zai yi.
Ya same ni a daki bayan tafiyar Usman cikinn halin kuka, ya tsorata mutuka, ya dagoni yana tanbayata dalili, ce masa na yi kaina ne kurum ke mini wani irin ciwo.ya kawo min magani ya bani a baki, sannan ya kwantar da ni.
Cikin dare na farka naganshi zaune, na dafa shi,lafiya Yaya?
Ya ce, Sadiya, ina ganin har in mutu ba zan daina nadamar laifin da na aikataba, ina cikin dana sanin zinar da na aikata da banyi ba da ban fada cikin wannan halin ba, yanzu tunanina da wane yare zan fahimtar da Iya cewar zan auri wannan yarinyar? Tsoron tunkararta nake da zancen Aunty wallahi,ban san me yasa a duk lokacin da mijina ya shiga damuwa hankalina kan tashi tausayinsa ya cikani,gaskiya da mutane suke cewa In kana son mutum kana tausayinsa. Sai na kwantar da kaina a kirjinsa, sannan nace. Don wannan Yaya Kar Ka damu, in Allah ya kaimu da safe zan samu Iya, ko kuma muje tare da kai. Ya ce, Sadiya bana son yadda nake ta saki karya don ki fitr da ni. Na ce, Allah zai dubani ya yafe min karyar insha Allah, tunda dan gyara nayi ba don

batawaba,Ya rungumeni yana fadin, Sadiya Ke ce rayuwata, Ke ce abar alfaharina. Na ce, nima kaine rayuwata. Muka kwanta cike da damuwa a zukatanmu.
Goma tagota muka fito zuwa gidan Iya. Yayaya yi mutukar kyau cikin shadda waganbari mai kalar sararin samaniya(sky blue), Hula mu hadu a banki,itama kalar kayan, wanda kyan shi ya tona tsadar shi, yana ta kamshi. Ni kuwa Atamfa na sha Purple mai ratsin fari, Takalmi da Hijabina kuma farare, muka jero tamkar sabon aure muka nufi gidan Iya.
Tana zaune kan sallaya ta idar da salar walaha da fara'ar ta dubemu tana cewa. Masha Allah ina zaku haka tabarakallah amma kunyi kyau. Muka sa 'yar dariyar yake dan nayi Imani yadda nake tsananin fargaba, hakan nanma Yaya yake ciki. Nace gurinki muka zo. Yaya ya ce daga nan za mu je kasuwane ne sai muji ko kina son wani abun?. Ta ce, bana bukatar komai Gadanga. Duk wani abu da zan nema ka ajiye min, ga firji da ka sai min ina ta saida ruwan sanyi ina samun na batarwa, ba abunda nake bukata Allah ya shi muku albarka yasa yayanku su goyaku.Muka ce ameen,tace, yan uwnka sun zo sun fada min cewa ka kai musu kayan abinci su duka ko?yayi yar' dariya, 'Iya wannan aikin Sadiya ne, ta ce duk wata in dinga sai musu kayan abinci shi ne muka fara da wannan watan. Iya ta kalle ni da dariya, 'Hali Dubu rubutun dutse, halinki dubu duk na alkhairi, na san sai ke 'yata. 'Ta kalli Aliyu. Dadin auran mace tagari kenan zata dinga bai wa mijinta shawara ta gari. Aliyu ya dube ni, sannan ya kalli Iya, 'Wannan gaskiyane Iya. Nace, 'Yanzun ma gurin ki muka zo kan wani batu.....tace, to, ya aka yi? Na kalli Yaya, shi ma ya kalle ni na ce, 'Ka fada mata. Ya ce, 'A'a ban san ta inda zan fara ba ki fada mata kawai in ta amince shi kenan. Iya ta ce, 'Ku fada min mana, kun daga min hankali. Na sunkuyar da kai, 'Iya dama mun yi shawara da Yaya ne a kan cewa zai ....za ya... 'Sai na yi shiru. Ta ce, 'Inajin ki. Na ce, 'Zai auri bakuwar nan ta gidanmu sabida tana

da hankali kuma.....' Da tsawa ta katse ni, 'Ke! Da kata kin san me ki ke fada kuwa? Waye zai auri wa?
Na kalle ta 'In..
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Yaya ne (Na nuna shi) zai auri Mujidat, tana da hankali Iya sosai. To ya ce yana son kara aure shi ne na ce ya aure ta. Iya ta rabka salati,sannan ta ce, 'Amma ban taba sanin ke mahaukaciya ba ce sai yau, ni ban taba jin inda aka ce ga wata mace ta ce mijinta ya yi mata kishiya? Ta sake zabga salati tare da riqe haba tana kallona. 'Ko ni nan da nake tsohuwa bakeba a ce babanku zai dawo duniya zan amince ya yi min kishiya? Dan haka ban yarda ba. Muka kalli juna da Yaya, ta ce, 'Meye matsalar ka da har kake son kara aure? Ko har yanzu bata son haihuwar ne? Ya ce, 'A'a wallahi bata da laipin komai kuma ba inda ta kasa, dama sabida raya sunnah ne kamar yanda yake cikin musulunci, yarinyar nan kuma Iya ta musulunta ne in ta auri wanda ba na kwarai ba za ta dauka haka halin musulmi yake, amma mu za mu yi mata mu'amula ta kwarai yanda ba za ta yi da ta sanin musulunci ba. Iya ta ce, Eh, ai dama ke Sadiya ba a yada ke gurin magana,ni fa dan ke nake fadan nan amma ke na lura kamar zuga ki nake, wai ke ba kya kishin mijinki ne?nayi 'yar dariyar yake, sannan na ce 'Ina kishinsa mana amma hakan ba zai hana shi ya kara aure ba. Ta yi shiru tana kallon mu can ta ce, 'Ni fa ban yarda da yarinyarba, kallonta nake kamar wata 'yar bariki ko wadda ta buga duniya. Muka kalli juna,Ya ce, 'Ai kin san zaman Lagos, sannan ba ta dade da Musulunta ba.Nace, 'Eh, ba ruwan ta Iya. Ta ce, 'Oho! In ma da ruwanta ke ki ka sani tunda kin ji kin gani ai shi kenan, ni me zan ce, Allah yasa alheri. Yauwa, kwanaki yayanku kece min 'yan uwanta sun zo na ce shi ne don

rashin mutunci ai sazo su min godiya. Muka sake kallon juna ni da Yaya, na ce, 'Af wannan laifina ne Iya ni ce ya kamata in rako su kiyi hakuri. Ta rike baki tare da cewa, 'Uhum! Abind ya same ki kar Allah yasa ya samu sauran dangi. 'Na ce Iya na gode bari mu tafi. Haka muka bar Iya baki bude tana mamakina,ni kuma na ce masa mu tafin dan kar ta canza ra'ayi,duk da ta amince, amma ba wai ina murna ba, bani da yanda zanyi da ya wuce in kauda da kai a yi auran, na san mata da yawa za su ga baike na amma ina san su sani DA KISHIYAR WAJE GARA TA GIDA.Daga nan gidansu Anty Abida ya ce mu tafi,,ni dai muna tafe ne ba kamar yandamuka taho dazu ba, ba wata hira bare annuri. Mun samu Usman a gida don haka muna shiga suka fita. Aliyu ya kalli Usman 'Aboki, Iya fa ta yarda da batun Mujidat. Cikin mamaki Usman ya kalle shi tare d fadin, 'Kai haba? Aliyu ya ce, 'Allah da gaske. Usman ya ce, 'Banzata ba, ya aka yi ta amince da sauri haka? Ya ce, Kai bari kawai,yarinyar nan Sadiya aboki ba ni d abind zan biya ta, ita ce ta shawo min kan Iya har ta amince da batun,sai na lura da akwai wasu shakku daga zuciyarta, Allah yasa ba ta gane cikina Mujidat ta haifa ba.Usman ya ce, 'Ka kara rike matarka da kyau,ina fada maka a wannan zamanin ba za ka samu tamkar ta ba, ina fada maka ko Abida matata ba za ta yi wannan jan aikin ba, tana fada min sai dai ta ce tana karfafawa Sadiyane dan tasan za ta iya kuma hakanne mafita. Aliyu ya ce, Allah ya ba ni ikon riqe ta da gaskiya. Usman ya ce, Ameen, yanzun mu tafi gidan su Yaya Sulaiman mu ji yanda za a yi. Aliyu ya ce to, Allah ya rufa asiri. Abida ta dube ni ina kuka, kallo na kawai take yi bata hana ni ba kuma bata bani hakuri ba. Sai da nayi mai isa ta. Sanan na share hawaye na, sanan ta dafa kafada ta. Sadiya kada kiga cewa ban baki hakuri na barki ne ki rage radadin dake zuciyarki, gaskiya ne in ka zubar da hawaye yana rage bakin ciki, amma in tambaye ki mana? Na kalle ta da jajayen idanuna, ta ce kukan nan na menene kike yi? Murya ta a dishe tana rawa na

ce, anty... Abida ina da matukar kishin Yaya Aliyu,Dan ban san irin son da nake yi mashi ba, kukaba yakunshi abubuwa dadama, amma kishin mijina shine a gaba, wai mijina zamu raba da wata, inna tuna haka hanjina na kaduwa, da na sani ban amince ya aure taba.... Sabon kuka ya kubuce mun.Tace kijure, Allah yasan nufinki, karki bari yaga karaya daga gareki, domin ba mijinkiba har mijina ya ce kin burge shi kullum cikin yabonki yake tare daba mijinki shawarar cewa yayi maki kyakkyawar ruko, dan haka ki cigaba da dannewa. Na ce, to anty zan kula, yanzu na sha kanshi ya amince in nemi koyarwa, sai dai ban san ta ina zan fara ba. Ta ce kada ki damu shugabar makarantar firamare ta L.E.A unguwar Mu'azu kawar yaya ta ce zanyi mata magana sanan karamar hukumar Kaduna ta kudu ma babban wan su Usman yana gurin ne kuma nasan zai tai maka. Na ce, to, aikuwa nagode Anty Abida Allah yabar kauna. Tace amin. Haba ai ba komai wallahi. Nan muka wuni nakasa cin komai, Anty Abida har Dan wake tayi min wai taga inaso, amma da kyar naci uku ina taunawa tamkar ina tauna magani, ko ruwa na sha sai inga tamkar magani . Anty kanta ta shiga damuwa tana min fadan kan in kashe kai na a banxa. Na ce mata. Anty kiyi hakuri cikin kwanakin nan ko gida na bana iya cin abinci in na dauki littafin marubutan nan in dan duba sai komai ya tsaya min inkasa fahimtar me nake karantawa mai makon in karanta litafi sai dai shi littafin ya dinga neman karantani da ko ina da yar matsala inna karanta sai ya dan rinka debe min kewa. Ta ce ai duk ki ajiye batun littafi kirumgumi mai kankat wato, ALKUR'ANIR KAREEM. Na sauke ajiyar zuciya,, tabbas Anty Alkur'ani yana sanyaya zuciya mu kan musalmi bamu da kaico sai godiya ga ubangijin da yayo mu a musulmi. Ta ce haka ne Allah kasa mu mutu a cikin musulumci muna a musulmai. Na ce amin.

Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com

Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Kafin su dawo ta sani na wanke fuskata nayi yar kwalliya, duk da fara'ar da nadingayi sai da yaya ya gane nayi kuka, duk lokacinda na kalle shi sai in ga idanunsa na kan fuskata har dai ya kare ya ce Sadiya kukan me kikeyi? Muka kalli juna da Anty abida ta ce, sam bata yi kuka ba me kagani? Yayi dan yake shi dole murmushi, ko ba jami'in tsaro bane ni, kun san daini ba yaro bane. Na share zan cen da cewa, yaya mu tashi dan yara na jira na in daukosu. Ya ce madan saurareni. Abida ta kalle shi ya ce, nifa bana son abin da zata shiga matsala, in auren nan zai kawo mata damuwa wallahi sai a fasa duk abin da zai faru ya dade bai faruba kowa ya ji cewa nayi wa wata ciki ta haihu, daga nan fa? Na runtse ido, don Allah yaya mu bar maganan nan, nace maka ba damuwa nake ciki ba, ka yarda dani. Usman ya ce aboki ina ga dai na dawowa da hannun agogo baya din nan a bar shi. Abida ta ce ai sadiya jaruma ce bata cikin wata damuwa, kuma malamai sun sha fada muna cawa in Allah ya rufa maka asiri yayin da ka aikata wani laifi to kai kada kayi kokarin tonawa kan ka don haka barin batuna haka shine mafi a a'ala. Haka dai muka baro gidan nasu bayan sun yi mana rakiya.
Saty daya bayan nan suka shirya tafiya lagos, sai dai ban da ya Sulaiman saboda suna son yan da haduwar su da dangin mujidat zai kasan ce, haka nan basa son yanda ya Sulaiman ya san cewa dan da ta haifa na shi ne. Sun tafi da Usman da shi Aliyun da kuma Mujidat da Danta. Sai dai lissafin da aka yi masa ya same wuce hankali, domin ko auren Sadiya bai kashe wannan kudin ba, sannan kudin sa da ke accout yayi shirin siyan wani gida ne da aka yi masa tallansa can kasan su a sabuwar unguwa da ke nan unguwar Mu'azun. Ya kalli Usman ya ce aboki ni fa ba zan iya biyan wayan nan kudinba. Usman ya ce, to ka kirata ta fada musu baza ka iya yin al'ada ba. Ya kalli

waliyin ya ce a kirata. Sai suka ce ai su al'adar su ba a magana da amarya sai su waliyanta. Usman ya ce to su basa yin wanan al'adar sadaki kawai zasu biya. Sauran suka ce sam ai tunda ta haihu a tasu al'adar yin biki dolene, kuma abubuwan al'ada dole ne, domin ita mai albarka ce mai haihuwa ce, sannan ba dama ya ce ya fasa tunda ta haihu.
Shi da Usman suka kalli juna a ran shi ya ce lallai ya debowa kanshi ruwan dafa kanshi. Usman ya ce kawai ka basu inya so sai ka sai fili bana son a samu matsala. Nan dai ba da son ran shi ba ya amince bayan sun fita suka tafi banki in da ya ciro kudi suka dinga yi masa lissafi yana ba su, nan fa suka ce jibi za su yi hutu, suka amince a haka. Ni kam ko da suka dawo bai fada min ba gurin Anty Abida na samu labarid Usman ke fada mata, na ce shi dai ya sani can da yawarsa.
Idanu na zuba ina kallonsa yau da na ga yanzun yana dan zakewa tare da rawar kai, sam ban zata ba, ya sa a yi gyaran gida. An yi fenti na kwashe kayan yarana daga dakin da ta zauna tunda nan za'a sa ta, ya ce da ya so canza min gado,amma in yi hakuri ko daga baya ne. Yaba ni dubu talatin,na yara ashirin na karba na aje tare da cewa mun gode. Na dauki waya ta ina dannawa ya ce, Wai Sadiya akwai wani laifi da nayi makine?na kalleshi' Me ka gani? Ya ce, Na ga tun jiya da na zo ba wata fuska a gurinki?Na maida kaina ga kallon wayata,sannan na ce, Akwai abin da ban makaba daga cikin wanda na saba yimaka?Yace, A'a,kin min komai MY CHOICE, sai dai ni na gane kamar ba ki da walwala. Na ce, Ba ka yi min komai ba. Ya ce, To anjima zan tafi, Na ce, Allah ya kai mu. Har ya kai bakin kofa na ce, Au! Na manta in fada maka an dauke ni amma ba aprimary ta nan unguqar Ma'azu ba, ta can Tudun wada. Ya tsaya yana kallona, nima shi nake kallo don son jin ta bakin shi,a zuciyata ina cewa yanzun dai a ce ya hana ni, tabdijan! Da sai ya ji magana. Tamkar ya sani sai ya ce na san kina zaton zan hana kineko? Ai ba ni da yanda zan yi tunda na rigana yi miki alkawari,amma ki

sani raina baya so. Ban ce kala ba na ci gaba da danna wayata shi kuma ya fita.
Ban tabbatar da cewa ina da kishi ba sai da lokacin auran ya gabato,wallahi ko abinci kasa ci nayi duk datausar da Aisha ke min da kuma Anty Abida dan ganin na kwantar da hankalina, amma na kasa, bana bacci sosai duk da cewa bana nunawa Yaya damuwata sai dai shi duk lokacin da muka yi waya sai ya yi min korafin in daina damuwa in kwantar da hankali,To kurum nake ce masa, amma zahirin gaskiya zantukansa ma soya min rai suke yi.
Ana gobe daurin aure zasu tafi can Lagos din ina kallo shi yana ta shige da fice yana shiri,an zuba sababbin dinkuna an sai Huluna da Takalma sai ina mamakin mutumin da na dinga shan kan shi da kyar shi ne yake zumudi. A fili na ce Allah yasa abin ya tsaya nan. Ya fito cikin shiri ina kwance kan gadon yara ya ce 'My Choice mun shirya,na dago na kalle shi, yayi matuqar kyau cikin Shadda Wagambari Blue shar kaladaya da hularsa mu hadu a banki, kamshinsa ya cika gidan, kishi ya kama ni mai tsanani,na kau da kai gefe. Ya ce, 'My choice yaya ne? Ban tanka masa ba sai zuciyata ta ce gwada shi ki gani da yake cewa in na ce ya fasa zai fasa,in ya so duk ma abin da zai faru to ya faru. Ya tallabo fuskata.
'My Choice, yaya ne? Na ce, 'Ni fa gsky na sake tunani a kan wannan auran, gaskiay ina tsoron abin da zai biyo baya. Zai fi kyau a barshi.
Zumbur ya mike tsaye daga russunawar da ya yi, na kalle shi ga mamakina fuskarshi daure, ya ce, 'Me ki ke nufin maidani? Karamin mutum? Kin sa mun yi magana yanzun kuma kizo ki ce ke kina jin tsoro, ya kamata ki fadi haka ne tun kafin yau, sai dai ki yi hakuri,mamakida tsoro suka sa na kasa daina kallonsa sannnan ga hawaye yana ta zuba tamkar an bude famfo, na girgiza kai tare da sauke ajiyar zuciya,sai kuma ya zauna kusa da ni tare da dafa kafadata. My choice bana nufin cutar da ke kece kika karfafani kika nuna min yin auran nan shine mafita, to me zai sa yanzun ki bijiro min da wani sabon batu bayan

aski ya zo gaban goshi? Kuka ya kwace min na shiga rera shi, tsam ya makaleni jikinsa yana lallashina. Sadiya in kin ce baki so wallahi abar shi. Ya ciro wayar shi yasoma dannawa. Bari na fadawa Usman ya kira Yaya Sulaiman ya fada masa cewa nafasa.ina jiyo shigar wayar ta soma ringing a can,da sauri na dago na amshi wayar da sauri na katse. Ya ce, yaya kuma za ki katseki bani in dakatar dasu su daina shiri. Na cecikin shagwabar kuka, Ni fa ban ce ka fasa ba.yasa hannunsa ya dago fuskata,To me kika ce?Na kalli cikin idon shi 'In ka aure ta zaka daina sona? Sai kurum naji bakin shi cikin nawa, minti1muka dauka, sai wayarshi ta shiga ruri,ya sakeni tare da daukar Wayar. Usman ina zuwa. Ya katse ya kalleni. My Choice in na yi rantsuwa bazan yi kaffaraba Ke ce 1 tak nake so, kum na soma son ki ne tun Ikcn da kika soma zama mace. Da farko ban fahimci ina sonki bane sai da Usman ya kwadaita mini da nazo iya ta ki sai na samu kaina da kasa hakura, wannan ya tabbatar min cewa ina mutukar sonki,Ke ce zabina, kada ki damu da Mujidat sam ba na son ki hada son ta da naki, Ke ba ita ba in miki ta mahaukaci duk duniya ba wata mace da nake so ko kuma zan sota sama da ke, ki rike wannan a cikin zuciyarki,so 1 tak Ke na ke yiwa shi.,lumshe ido na yi inma karya Yayaya fada min to na yarda don gaskiya maza da ace zasu gane furta son ka ga matar ka komai dadewar aurenku yana susutar da mace komai shekarunta ta ji ta tamkar sabuwa,amma matsalar maza musamman irin na yankinmu ba sa iya cewa matar su suna sonta, ko wasu kalamai na soyayya irin wanda suke yi mata yayin yakin neman aurenta da zarar sunga cewa sun aurenta shi Kenan ta tsufa Nima haka na ji tamkar farkon aurenmu duk damuwar dake cikin zuciyata sai ta gushe, sabida ina son a so ni,ina son a nuna min soyayya, ina son a fada min kalaman so. Nasa hannu a kumatun shi na shafa ina kallon cikin idon shi, Yaya na gamsu da kalamanka, Allah ya tsare hanya gobe zaku dawo? Ya ce, insha Allah ko jibi, tunda da nisa in

mun taso da yamma ko da dare sai safe zamu iso. Na ce shi Kenan. Ya mike tsaye, me zan sayo miki a can? Na ce, gdnsu lesuka, in ka siya min zanyi murna. Ya ce insha Allah zan zabo miki masu kyau. Na ce to nagode. Har waje na raka shi. Sai dai duk da haka kasa bacci nayi daren ranar sai damuwa da sake saken zuci.
Washe gari kuwa data kasance ranar daurin aure ba zan iya lissafa tashin hanklin da na shiga ba. Da safe kasa zama na yi a gidan na tafi gidan Iya wai don in manta da batun auren amma duk da haka na kasa sukuni, har Iya ta fahimta, sai kurum naji ta ce. Sadiya, hakika kishi wani abu ne mai rai, amma yana da sauki in kin saukakashi, ina son ki nutsu ki rike girmanki. Shawarar da zan baki ki kara zage damtse gurin kyautatawa mijinki kada ki dauki halayen wasu matan masu cewa in miji ya kara aure zasu daina yi masa komai suce ya je can matar da ya auro tayi masa, wannan kuskure ne, don in aka samu wadda ta san hannunta kafin ki samo mijinki sai wani ikon Allah,ki zama a gidanki Ke ce uwar kowa. Ina nufin duk abinda ya taso na kudi ko matsalar lalacewar wani abu a gida Kar ki tsaya jiransa kiyi da kudinki in yaso in yazo kya karba ko yaturo miki, sannan ba'a fata in har sabani ya shiga tsakaninki da ita tunda an ce zo mu zauna zo mu saba, to kada ki sake ki fara kai kara Kinji ko? Na ce, to. Yauwwa sabida in kinyi nazari cikin ya'yanki mai yawan kawo kara duk gaskiyarshi sai kinji haushinsa. Na ce, haka ne. To ki rike hakuri da addu'a ki dinga yawaita karatun Alkur'ani mai girma, ki zauna da ita zuciya1, sannan ga aikin ki ma, ai ni naji dadin barin ki da yayi wannan koyarwar, na ce, nima naji dadi iya, don ina da yara gara dai yanzu da muke mu 2 aikin ya dauke masa matsalolina in ina samu ba sai na jira shi ba, kudin da ya bani ma nawa da yara wai muyi siyayya su dai na Dan sai musu wani abu, so nake in hada jari in dinga saye da siyarwa. Iya tayi dariya tare da cewa, da kyau Sadiyayyena. Haka nayini Iya tana kwantar min da hankali tare da bani shawarwari sai kusan 10 na dare na debi

ya'yana ta raka mu har gida, nima na sake rako ta hanya.ina sa hakarkarina a kan gado na dauko wayata nakunna dama yinin ranar kashe ta na yi. Nan fa sakonni suka soma shigowa na yaya sai na Aisha da Anty Abida, na su na soma dubawa. Tanbayata suke ina naje sun zo ba nanan? Na yi dan murmushi, a fili na ce da kun zo gidan Iya ni kam ba zan yi wani taro ba, sai na soma duba nashi,duk kusan yana nuna damuwane akan ya kira bai sameni ba. Sai na karshe da yake cewa sun taso 9 suna hanya, akwai yiwuwar su iso kafin 9 na safe, kuma suna tare da wasu daga danginta dan Allah ta tanadar musu abinci. Kiran Abida ya katse karatun sakon da na keyi, na daga muka gaisa, ta ce min, ina na shige yau? Na ce ina gidan Iya,tace to, ki yi sammakon tashi don mijinki zasuyi shigowar safe ne, nace Anty me zanyimusu?tace karin kumallo mana kiyi zuciya1 kada ki sa kishi ciki, bakin kine, kin kuma san darajar baki a musulunci. Na ce to Aunty zanyi.
Tin 4 na tashi na fara firar dankali da nayi sallah kuma na hau suya, har kaji biyu nayi musu farfesu, kwai ma isasshena yi musu kwai da kwai na dafa ruwan tea mai yawa, sannan na gyara gidana nayi wa yara wanka na zabo musu sababbin kaya nima na sheka nawa adon.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Takwas daida na ji tsayawar motoci,gabana ya yanke ya yi wata muguwar faduwa,sai na hau karanta Hasbunallahu wa ni'imal wakil. Na mike na je na bude musu kofa gabana yana ta faduwa,zuciyata tana maimaita addu'a.suka shigo suna yi min sannu, wasun su suna kallona wani iri,amma duk da haka na saki raina ina yi musu sannu da harshen Turanci.Najee na bude musu dakin suka yi sororo a tsakar daki don ga al'adarsu miji ke shiryawa mace daki ya zuba komai, ita kuma iyayenta su yi mata kayan sawa,

nan fa suka soma yare, duk da bana ji amma ganin yanda suke magana suna tabe baki na fahimci zancen nasu bana dadi ba ne, naje nasoma fito musu d kuloli. Sai gasu Yaya sun shigo, na kirkiro fara'a ina yi musu sannu da zuwa. Falo suka je suka zauna na gabatar musu suma da abin kari, na kula yaya ya ji dadin yanda na saki jikina na kuma yi musu abin kari.Nan nabarsu nayi daki,bayan Mujidat da danginta sun gama karyawa sai suka samu su Aliyu da Usman suna yi musu korafin ba su ga kmai a dakin ba.Usman ya ce, Mu a nan da kaya amarya take zuwa. Suka ce su kam ba haka ba ne, nan suka fito masa da akwatunan amarya har da na mijin da na Maman shi da kuma na danginsa. Aliyu ya ce shi kenan zai siya daga baya, amma yanzun a kwaso na dakinsa a sa mata,sukace bakomai. Ina dakin nashi ya shigo wanda zuwa yanzun ya zama nawa,ya zauna. Sadiya kin ji wata sabuwa. Na kalle shi, ya ce, Wai ni zan sai mata gado. Na ce, ina zaton haka al'adar su take don mun taba yin zancen da wata 'yar ajinmu da muka yi N.C.E take ba mu labarin al'adunsu, miji ke yin kayan daki kuma sadakin su yana da tsada, amma mace za ta ja jari da su ita ce za ta rike gida,wasu kuma jarin daban miji zaibada, wadanda ba Musulmi ba sun fiyi, Musulminsu kamsai sunyi aure suke tarewa gidan mazajensu,yace,nidai yanzun ya za'a yi? Na ce su zo su dauki wannan gadon. Na tsura masa ido cikin mamaki,sai ya ce, ko ya ki ka gani? Na mike na nufi dakina bayan na ce, Me zan ce kai da abinka. Na shiga dakina na soma kallon dakin ina lissafa yanda zan gyara shi ni da yarana da na bar musu gadona tunda dama katifu gare su. Sai ga shi ya shigo.Haba Sadiya,me zai sa ki yankemin wannan hukuncin? Nazo miki da shawara amma sai ki yi watsi da ni kitaho abin ki? Na ce, Yaya kainefa da abinka kuma ka ba matarka, mene ne laifina dan na taho? Yace, Ok, kije amma ki sani kada nan gaba ki ce na daina kawo miki Shawara,kin sani dai ke ce kurum nake tunkara da duk matsala ta. Shiru na yi dan nasan

in hakan ta faru lallai ba zan zama uwar gidaba. Ya mike zai fita na ce, Yaya" ya dawo,Mene ne? Na ce, Shi kenan ka yi hakuri. Ya zauna tare da kamo hannuna, Nagode da ki ka fahimce ni, yanzun ya ki ke ganin za'ayi? Na ce, Ka ba ta,ni kawai sai naringa kwana a nan da yarana. Ya tsura min ido, To nifa? Na ce, Ba komai ka yi ta kwana dakinta. Ya yi dan murmushi, Har yanzun baki huce ba.Na yi 'yar dariyar yake, Bana fushi da kai. Yace, Zan siyo katifu yau a sa can dakin in komai ya warware zan canza gadajen gidan.Na ce to maimakon ka ba ta tsohon gadon ba gara ka sai mata katifar ba? Amma yanda ka gani, Ya ce na riga na fada musu ne na ce to su dauka bari. In zo in kwashe kayan na wardrobe din. Ya ce, A'a, gado kawai da katifa za ta dauka. Na ce, Shi kenan, Allah ya rufa asiri. Ashe tashin hankali yana gaba,sai lokacin bacci, Mujidat ta kira shi a waya wai tana jin bacci, ya kalle ni muna zaune kan gado,sannan yaci gaba da magana. To ki kwanta mana. Ta ce, Ba dakin ka zan kwana ba? Ya ce, A'a yanzun bani da daki in danginki sun tafi na kwana adakinki. Mamaki da haushi suka cika ni, ga kishi kamar in hade raina, na ce, Kuje dakin naka mana? Yaja tsaki tare da cewa, Don Allah ki bar wannan maganar. Na kwanta tare da juya bayana na rungume yarana bankara sauraron shi ba, shi ma ya kwanta a daya gefen

Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com Kokuma ku kasance taredamu a facebook https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Washe gari tun Asbahi suka soma shiri,suna karyawa suka tafi, wata daya ce daga cikinsu kadai ta yi min sallama da godiya, suna kama ina zaton yarta ce dake illorin din, domin nayi dawainiya dasu sosai ta fannin abinci. Ya tsaya da su sun shiga gurin Iya sun gaisa duk da cewa ba sa jin yaren juna, sannan ya wuce dasu zuwa gareji. Ranar ne matan Yaya Sulaiman da su Anty Abida sukayi ta zuwa ganin Amarya. Anty Abida

ta yi ta yi min fada wai ya zan sa abu a cikin raina ga shi nan duk na rame, na ce Anty dole in sa a raina, ba za ki fahimci zafinkishi ba, duk irin bayanin da zan yi miki, kuma bana fatan a yi miki ki ji.Anty Abida tace, Ameen,don Allah ina son ki saki ranki. Amarya dai tana daki bata fito ba, da za su tafi na raka su ganin amarya ta ci rigarta da wando na bakin Jeans, danta yana cikin gadon shi ta yi ruf daciki kan gadon da suka kafa tana chatting, a yatsine ta amsa sallamar,sannan aka gaisa,suka yi fatan alkhairi suka fita.
Daran ranar ne ya hada mu a falo yana yi mana nasihar zama lafiya, sam ban san me yake cewa ba, ina can gurin tunani. Yau ga shi abin da nake karantawa cikin littattafai ya zo kaina, ji nake tamkar cikin mafarki, ashe dai nima za a min kishiya. Girgiza nin da yayine ya sa na dawo cikin hayyacina,cikin damuwa ya ce, Menebe? Na girgiza kai ba komai. Ya ce, ina tambayar ki game da kwana,na ce, Nawa nawa? Nayi hamma kirkirarra, sannan duk yadda kace. Ya ce, To a bar shi bibbiyu kamar yanda aka fi yi. Na ce shi kenan. Ita dai tana ta jijjiga danta,na sake kirkiro hamma, zanje in kwanta bacci. Ya kalli agogon bango; Da wuri? Na ce, Na gaji ne. Na kalli amarya wadda ta sha leshi kai ya ji gashin doki ya zubo har kafada, na ce, Sai da safe,ta dube ni da 'yar yatsina eh, dama ban jira amsar ta ba na yi tafiyata. TABDI! Daran ranar kasa bacci na yi har zuga ni zuciyata ta dinga yi wai inje in labe inji me suke yi, amma sai na fi karfinta inda na yo alwala na yi ta sallah in nagaji in dauki Alkur'ani nayita karantawa,sai da na yi sallar Asubahi sannan na kwanat. Allah ya taimake ni yarana suna cikin hutun makaranta ne, don haka da na tashesu muka yi sallah sai muka koma. Ban farka basai tara, ina tashi Mama ta tashi, sai da na yimusu wanka sannan muka fito.....zandakata anan zuwa lokaci na gaba,fatan zaku kasance tare dani
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com Kokuma ku kasance taredamu a facebook

https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Zaharaddeen Shomar
Whatsapp  08168575100

Darajar Yayana3-04
Posted by ANaM Dorayi on 07:21 PM, 06-Apr-16
Under: DARAJAR 'YA'YANA
__________________NA
___________HALIMA K/MASHI
Tun a falo nasan cewa masu gidan sun jima da tashi,domin ga gurin da aka karya nan ba a kwashe kayanba,na shiga kicin na soyo wayara dankali da kwai, dama ni ban damu in ci wani abuba don bana jin yunwa, na hada musu Tea sannan ni kuma na sha ruwan Lipton, na kwanta ringine ina karanta wani post da Sheik Daurawa yayo a facebook, sai ga shi ya shigo, idanuna basa san kallonshi, ina jin su Kausar suna gaida shi ya amsa tare da sumbatar su a goshinsu su duka, sannan ya zauna bakin gado kusa da ni. My choice,ina ta shigowa kuna bacci da yaranki. Ban tanka masa ba ya ce, An tashi lafiya?
A ciki na ce, Lafiya lau. Ya ce, ke kin ci abincin ne? Na ce Um, ya yi shiru yana tunanin me zai ce, ni ko da zai fita ma zan fi so. Sai ya ce, yauwa am, Sadiya jiya namanta ba mu yi magana ba. Ba tare da na dago ba na ce inajinka. Ya ce yanzun wane hukunci zamu dora Mujidat ko in ce ina za mu ajeta? Budurwa ko bazawara? Yana cewa haka na fuskanci nufinshi wato kwana nawa zaiyi, zuciyata ta soma tafasa,amma sai na fara karanta addu'a, na tashi na kalle shi. Mujidat budurwa ce, don haka sati daya za ka yi a dakinta, garabasa ma dazan yi maka ita ce ka gama hutunka kaf a dakinta. Ya ce, a'a ban yarda ba. Na koma na kwanta ba tare da na kara cewa komai ba. Ya amshi wayar hannuna yana cewa. Me ki ke gani

ne cikin wayar ki, wanda ya fi ni? Juyowa na yi ina kallon shi,sai da ya gama karantawa,sannan ya ce, Banace kirufe wannan account din ba? Bana son kina hawa facebook fa. Yayi maganar tare da dan hade rai. Nace, To ni menakeyima a facebook din? Daga ganin abin da duniya ke ciki sai post din malamai,sai ko gidajen da akabude dan wayarwa da mata kai. Ya ce, Duk da haka dai na ce ki rufe zan sai miki kasunan wa'azi in namu sun miki kadan, sannan zan baki kudi ki sai littattafai na wayrwa da mata kai din, huldarki da internet din ne ba na so,ban amsaba,shi kuma ya fice. A raina na ce ka zaci abin da kakeyi a internet din haka kowama keyi? Na ajiye wayar batare da na goge ba, sai dai cikin zuciyata na dauki aniyar gogewa,amma ba yanzu ba. Duk zatona da naganta kicin tana girki duka gidan za ta yi, amma sai na ga ta juye kula daya ta nufi dakinta, don haka sai na tashi nayiwa yarana.

Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa

Anamdorayi.mywapblog.com

Kokuma ku kasance taredamu a facebook

https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Bai shigo gidanba sai Magriba duk da dai ya kirani ta waya da rana yace menadafa? Na ce masa taliya, shi dabagwanin taliya ba ne don haka sai ya ce to bari ya ci tuwon sa gurin Iya. Ya sameni daki ina karanta littafin Hausa, su Kausar suna ta wasa, nan suka tashi suna yimasa oyoyo, na dube shi tare da yi masa sannu da zuwa. Ya amsa,sannan ya zauna. Kin ganni sai yanzun? Na ce, Eh, ina zaton wani aiki ne ma ya taso maka. Ya ce, A'a, wallahi gidan ne sam baya yi min dadin zama duk jina nake a takure, shi yasa naso in sayi wancan gidan ga shi duk na kashe rabin kudin.

Dariya ta subuce min cikin zuciya nace ai ba a banza aka kashe ba,tunda aure kayi, ko ba nan kudin suka wuce ba? Shiru ya yi tunda ya san

bai fada min cewa kudinsa sun wuce a gurin auran Mujidat ba, sai ma ya dauko wani batun. Yauma baki cemin lesukan nan sunyi kyau ba? Nace, Na fada maka mana, ka dai manta ne ko dai anan kakashe kudin? Da sauri ya ce, A'a ni ban ce ba. Wayar shi ta soma ruri ya dauka, sai na ji ya ce, Ke ina zuwa nafa shigo gidan. Ina jin haka na san cewa Mujidat ce, a raina naji zafi mijina wata ke kira kuma tana da damar yin hakan, jin hawaye na son zubo min sai na mike na shige bandaki tare da cewa, Bari in yo alwalar Isha'i.
A dakin Mujidat Aliyu ya zauna idanun shi yana kallon Abdul wanda daga jiya zuwa yau ya soma son dan shi, ita kuma tana kwance rufda ciki tana chating ya sa hannu ya amshi wayar, ta tashi zaune. Honey ban waya ta, muna hira a group dinmune, don Allah.Ya soma danna wayar yana dubawa,can ya dube ta, Har da maza fa na ga kuna hirar? Ta ce, Eh, ba za mu yi hira ba,'yan group din mu ne fa? Ya kashe wayar, sannan ya sa ta cikin aljihunsa, ta ce, Ban gane ba, amma kai ka sai min? Ya ce, Zan sai miki wata da wani sim din yanzun karkashina kike ba zan yarda ki yi hulda da kowa ba,tace Kana nufin har da iyayena,da sauran dangina? Aliyu ya ce, Bance zan hana ki hulda da danginki ba, amma sai na tantancesu.taja tsaki,sannan ta zauna cikin fushi, ya isa gabanta yasa yatsunsa ya damki lebenta, Kar ki sake yi min tsaki sabida yanzun ni mijinki ne yana da kyau kisan darajata. Taji zafin yanda yayi mata, har ta yi 'yar kara sannan ya saki ya kuma fita. Na yi hakuri tare da cijewa gami da kau da kaina game da Yaya da matarsa.Ranar da ya cika sati dayama nace nakara masa wani satin,amma ya ce sam ba ya so. Kafin hutun shi ya kare wani aiki ya taso don haka ya shirya komawa ya kira mu falo ya ce to ni zan tafi. Ya kalli Mujidat. Kada ki sake in dawo inji wata matsala ta faru, sbd in na ga sabon abu daga ke ne. Na dade dasanin wace ce matata,sannan duk abin da ki ke bukata ki tambayeta. Sai abu

na gaba bance kitafi ko'ina ba, don baki dakowa a garin nan, kin fahimta ko? Ta turo baki gami da bata rai,sannan ta ce yana yi mata gorin dangi kenan? Ya ce in kin dauka haka to hakan ne. Ya dube ni, Kici gaba da hakurin da nasan ki da shi,sannan ki kama girmanki, kamar yanda kikeyi, inda wata matsala ki sanar da ni,sannan yau kwanana daya a dakin ki tafiyar nan ta taso,ina dawowa zan sauka dakinki in yi kwana dayan da ya rage,sannan in koma gurin ta,nace, to Allah ya tsare ya dawo da kai lafiya. Yara ma ya sallame su, kamar yanda ya saba muka raka shi har mota,har da Mujidat din sabe da danta a kafada,duk da ba ta zo kusa da shi ba. Na ce,baka sallami Abdul ba.nakalli Mujidat, Ki ba Baban shi su yi sallama. Ya ce, A'a, bar shi kawai. Ya tada mota, sam ban so yanda ya yi ba,domin a gabanta ya rungumi sauran yara tare da sumbatar su, fuu! Ta juya ciki, tun kafin ya tada motar,nabita da kallo,sannan na kalleshi. Yaya ka daina haka, yanzun mun zama daya kuma wannan yaron ka ne kar ka gwada bambanci ko ka ce za ka yi kara dan ganin idona na san dai kana son danka,ya tada motar tare da cewa, Na tafi.Na ce Allah ya tsare.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Gaskiya Mujidat ba ta bukatar muyi zaman lafiya yadda take mu'amalarta da yarana amma ni na sawa kaina alwashin sai dai tayi da wani amma badaniba, duk da cewa na san ban girme ta ba,amma a gurina zubar da aji ne in tsaya cacar baki da kishiya,gurin cin abinci dama tun yana nan bai hana kowa yin na shi ba.Da farko na so in masa magana kan cewa ya za a ce muna gida daya karkashin miji daya, amma mu raba girki,sai kuma na ce bari dai in bar shi tunda shi ke nemowa.sai kuma ta tsiri fita zuwa

gurin wasu 'yarbawa yarensu,sai ta kai dare.
Randa ta fita na uku na yi mata magana,tana shiga dakinta na bita. Maman Abdul. Ta waigo ta dube ni,sannan ta ci gaba da kwantar da dan ta a kan gado. Na ce, Amma kin san mijinki ya cekar ki fita ko? Ta ce, Na fita din zan ta zama a gida ne? Ya amsar min waya,sannan ya cezai hana ni fita, ba zan iya zaman takura ba,nace,zaman aure shi ne zaman takura?
Ta ce, Maman Kausar don Allah ki barni kawai, kije ki harkar ki.
Jin haka sai na tafi na kyale ta.
Yaya bai zo ba har sati biyu,duk da yana kiranmuta waya ko yaushe yana tambayata ko akwai wata matsala a zamanmu da Mujidat,nace masa babu wata matsala, ina zaton bai fadamata cewa yana zuwa yau ba, tadaiga na haukace da aiki,munyo kitso da lallae ni da yarana. Ina da nacin yin lalle dan na san mijina yana matukar so, ya ce min shi zan tayi masa a gida,don haka su Kausar suna dawowa daga Islamiyya suka cire kayan makaranta na shirya su cikin sababbin kaya.Allah ya taimake ta tana shigowa ko minti goma batayiba na ji tsayuwar motarsa,nafito daga dakinsa inda na kai turaren wuta nace su Kausar ga Abbanku,da gudu muka fita ni da su, nan ta fito kallonmu, duk da cewa ko a da ta saba gani lokacin renon cikinta.Dukkanmu muka rungume shi,tsaki ta ja sannan ta juya cikin dakinta. Duk hidimar da mukeyi bata fito ba, har lokacin da muka shirya fita zuwa gidan Iya, na ce baka duba su Abdul bafa.Yace, Uhm! Yaushe nashigo gidan? Ni zan je in duba su koko suzasuzo duba ni? A nan na yi Magriba na yi Isha'i,ba ta fito ba,in ma za ta ce ba ta sanna dawo ba da Kausar ta kai mata tsarabar su ai ta san na dawo,nace, duk da haka ka leka,Tsaki yaja,sannan ya fita abinshi.
Na leka dakin, tana zaune bakin gado ta zabga tagumi ranta a bace, nace, Sai mun dawo za mu je gidan Iya,ga mamakina sai naga taja wani uban tsaki tare da banko min harara, sai na ji dariya ta subucemini, don haka na yi 'yar dariya

tare da sakin labulan nata, ina jiyowa ta yi wata kalma da yaransu wadda nake zaton zagi ne. Iya ta yi murna da ganinmu,sannan ta ce ina 'yar uwarki? Nace, Tana gida, ta ce a gaishe ki. Tace,Ina amsawa. Ita bata fitane bakuzo da itaba?Yaya ya ce, Ba za ta zo ba. Iya ta ce, Sadiya ke ce zaki dinga janta in zaki fita, don ta saba d mutane tunda kin ga ba ta san kowa ba. Nace to Iya. Mun je gidan Yaya Sulaiman, Yaya Zakari, da kuma Yaya Sani, duk mun ziyarcesu, inda Yaya ya yi musu alkhairi. Ina jin dadin yanda Yaya ke kula da danginshi suna shi masa albarka, sai dai bayamin kara yayi wa mahaifina.amma na sha alwashin koya masa.Daga nan muka dawo gida,kai har yanzun na tabbatar Yaya yana sona.sabida irin soyayyar da ya gwada min ta dare dayan da yayi a dakina. Washe gari mun yini gida cikin jin dadi da annashuwa, amma Mujidat taki fitowa, sai lokacin bacci sannan ya nufi dakinta.
Kuka ya sameta tanayi wiwi,ya isa kusa da ita ya ce, Lafiya? Ta watso masa kallon banza da manyan idanunta da suka kada suka yi jajir, ta ce, Haka dama aurenku yake? Ka nuna min cewa matarka kawai kake so, babiba. Ya ce, Menayi miki? Ta ce, Tunda ka dawo ka ajiye ni kamar kashi, matarka da yaranka kadai ka sani. Ya ce, Kece ki ka ja jikinki damu, na dawo kinki zuwa ki gaisheni.Ta ce, Ka fada min cewa zaka dawo? Sai na fada miki dole sannan zaki gaishe ni? To ni ba haka tsarina yakeba. Ta ce, Eh, amma ka iya fadawa matarka ai, tunda naga sun shirya,nima in ka fada min ai zan shirya. Ya ce, To shi kenan next time zan fada miki tunda dakin ki zan sauka, dan gobe zan tafi. Ta tashi ta dawo daf da shi tasa hannu a kumatunsa, Aliyu ina son ka da yawa, nima ka daure ka soni. Ya yi murmushi, sannan ya ce, Ina son ki mana, Ya kalli kitson ta. Har yanzu ba ki cire wannan gashin dokin ba? Bana son shi. Ta ce, To zan cire gobe. Ta dauko Abdul tasa masa a cinya.Tunda ka dawo ba ka dauki yaronka ba,ya kalli yaron cikin kauna, sannan ya soma yi masa

wasa da kumatun,sai dai koyaushe ya rike yaron gaban shi yana faduwa, kuma yana tuna masa cewa fa akwai wani asiri da ya boye. Ya kan ji tausayin Mujidat a irin son da take masa, kuma yana son ya kyautata mata ko don yanda ta hakura da rayuwar bariki ta yarda zatayi zaman aure,har inzata zauna da su lafiya to zai mata adalci, don haka ita ma ya nuna mata soyayya daidai gwargwado, wadda ita da kanta ta yarda cewa ya soma sonta.Haka nan da zai tafi ya sake tara muya yi mana nasiha,sannan ya tafi. Dama makarantar da aka dauke ni koyarwa sunce sai andawo hutu, tunda tuni sun min duk wani abini da ya dace kafin a dauki duk wani malami, don haka ana komawa hutu na soma koyarwa a matsayin sabuwar malama, aji biyu na nake dauka, wato 'yan safe. Don haka tun Asubahi inna tashi nake kammala yarana ina sauke su in wuce tawa makarantar, sai dai matsala daya aikin gidana dole sai na nemi 'yar aiki kenan. Kodanayi wa Aliyu wannan batun sai ya ce dalili kenan da baya san aiki ga matarsa, ba danbazai iya biyan 'yar aiki ba, a'a sai dan ba za a tsaya a duba masa gida da kuma yara ba. Na ce ni dai zan biya mai aikin cikin albashina, ya ce ai ba wai ba zai iya biya ba ne ya fi son ya ganni a gida.Iya na fadawa a samo min 'yar aiki,tace in kuna da wadatar gurin kwanane sai ku dauko Nasiba 'yar gidan Yaya Zakari. Na ce ai matsalar gurin kwanan ne, na fi son wadda ke kusa da gida,in ta yi aikin ta ta je gida. Iya ta ce haka ne. Ansamo min wata yarinya 'yar matashiya, kullum zatazo ta yi min wanke wanke da shara,haka muka ci gaba da tafiyar da rayuwa da dadi ba dadi, ina kuma yabawa Yaya yanda yake kwatanta adalci tsakaninmu, amma kullum Mujidat gani take yi Yaya ya fi sona da ita. Albashina na farko naje na sayo kayan abinci da zannuwa turmi biyu. Ranar Yaya ya dawo ya tsaya yana kallon kayan abincin.Wanna fa? Na ce, Babana zan kaiwa,tunda na yi aure ban taba yi masa wani abu ba. Ina kallon Yaya ya yi shiru yana

nazari,sannan ya ce, Nawa ne kayan nan? Na fada masa ya ce to kafin in tafi zan baki.Nace ayi haka Yaya daka barshi. Ya ce, Nima ai 'dan shi neko? Na yi shiru, ya ce, To zan ba ki ba zan so ba a ce kin riga ni kaiwa mahaifinki wannan alheirin. Na ce, To shikenan Allah ya saka da alkhairi. Ya ce ameen. Na ce, Ni dama ko da na kai da sunanka zan kai.ya ce, Yanzun ma duk ba haka ba,wai ke za ki je Zariyan?
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
na ce, Eh, wai da. Ya ce, 'A'a gobe zan je in kai musu. Na ce don Allah ka je da ni. Ya ce a'a,ina ce ke ce na ji Iya tana fada miki bikin kannanki guda biyu? Na ce cikin shagwaba, Allah Sarki Yaya bikin fa sai daf da Azumi akwai saura. Ya ce, Eh, ki hakura sai lokacin. Na ce, Shi kenan. To yanzun in kabani kudin nan me ya kamata in siya? Yace, Oho! Miki, ki bude account mana. Na ce eh, tozan bude.
Cikin wannan lokacin na soma rasa gane kaina, ba sai an fada min ba na san cewa ciki gare ni, ban taba irin wannan cikin ba mai masifar laulayi. Binta yarinyar da ke min aiki ita ce ke ta dawainiyar aikinta, har ma jinyata. Mujidat kuwa ba ta zama,bata taba yimin sannu ba, sai dai in jiyo tana ta yi wa yara wasa.Su Khausar su ne suka sanar da Iya cewa ba ni da lafiya sai ga ta. Ranar ita ce ta gyara min gida,sannan ta kira Mujidat tana ta yi mata fadan cewa. Me yasa 'yar uwar kina ciwo amma ba za ki taya ta aiki ba? Sai ta ce wai ita ba ta sani ba, ko da Iyan ta shigo tana fada na ce mata kar ta damu Mujidat ba mai son aiki ba ce, don ko dakinta ba kullum take gyarawa ba,Iya ta ce Allah ya kayuta, ni sai in gakamar ba kwa zaman lafiya? Nace, Lau muke ni da ban cika zaman gidan ba, don dai ciwon nanne. Iya ta ce, To kin sanar a

makarantar? Na ce, Har malamai sun zo duba ni. Ta ce, Allah ya kara sauki, ga shi kinki zuwa Asibiti. Na ce to ko na je ba wani abu da za su yi min sai magani, to ko maganin ba zan iya shaba, ko fa ruwa na sha sai ya dawo. Nan Iya ta yini kafin ta tafi..
Cikin dare kuma tamkar ba zan kwana ba, Kausar da Binta mai aikina sune a kaina. Kausar nata kuka,ta je ta fadawa Antynsu amma ta ki zuwa, tama ki bude kofa, duk da irin kwankwasawar da Kausar take yi, na ce su dau waya ta kira Babansu,sabida gani nake tamkar ba zan tashi ba. Ya daga kiran farko, Kausar ta ce, Abba, Momy fa ba ta da lafiya. Cikin muryar kuka ta yi maganar. Ya ce, tabani na amsa sannan nace sufita,suna fita cikin muryar wadda ke cikin matsananciyar jinya na ce, Aliyu ka yafemin bana zaton ciwon nan na tashi ne. Cikin daga murya na ji ya kirani da karfi, SADIYAA me ke damunki? Cikin rauni na ce ka yafe min? Bai amsa ba ya kashe wayar. Can jimawa sai ga Mujidat ta shigo, na san cewa shi ne ya kirata,ni dai daga karshe bansan me ke faruwa ba ma, ashe wai suma nayi.Ihun Mujidat shi ne ya sa su Kausar tashi daga bacci.ta kira shi tana ihu wai bana motsi,kila na mutu ne,ya kidime sosai da jin hakan kuma nan take ya kira Usman, yasanar dashi duk abin da yake faruwa, cikin daren Usman ya zo yana buga gida Mujidat sai tace da Binta mai aiki taje ta bude, cikin tsoro yarinyar ta ce waye? Ya ce nine Usman bude, ta bude. Har dakina Usman ya shigo, Mujidat tana ta ihu ya ce takama su sani a mota, ta ce ba mutuwa ta yi ba? Usman ya ce sai na ji daga likita.
Asbahin fari na farka na ganni a gadon Asibiti,an samin ruwa. Usman da Mujidat na gani tana zaune shi kuma yana jingine da bango,ya zo kaina yana min sannu, na kalli ruwan na gane ina Asibiti ne. Ya dubi Mujidat ta farfado. Mujidat wadda bacci yake fizgarta,ta ce uhm,uhum, tare da tabe baki,ta soma jijjiga danta, sannan ta ce, sannu Maman Kausar.

Idona yana lumshe kai kurum na daga,ina ji lokacin da Usman ya kira yaya fada masa cewa na farfado. Yace shi ma yanzun haka ya wuce Nasaraw daf yake da Unguwar Ma'zu , Usman ya ce muna asibitin Biba ne. Aliyu ya ce ka fada min. Yaya ya rude da ganin yanda na dawo,ya kama hannuna ya zauna bakin gadon, Sadiya me ya same ki? Na bude idanuna ina kallon shi ya rusuno ya sumbaci kumatuna. Sannu kin ji? Ya kalli Usman. Sannu Aboki, na gode Allah ya saka da mafificin alkhairi.
Usman yace , Haba dai sai ka ce wani abu? Allah dai ya ba ta lafiya. Aliyu ya ce ameen, na gode. Da ya samu labarin cewa ciki gare ni sai na ga Yaya ya soma murna,tamkar cikin fari. Usman neya taho da Mujidat wacce ke ta yin gyangyadi a zaune. Tunda duku duku sai ga Iya wai da Asuba Binta da Kausar suka je suka fada mata, ita ce ma ta tashe mu daga bacci, domin bacci ya sace mu Yaya na kan kujera ya dora kansa a gadon, hannuna yana kan nasa kawunan mu a hade, motsinsa shi ne ya tashe ni, suka gaisa ya fita sallah. Sai lokacin na tuna da 'yan yarana su kadai kenan su ka kwana.
Kafin yamma naji karfi sosai sakamakon ruwan da aka yi ta dura min mai dauke da sinadarin abinci,likitan ya sallamemu tare da ba mu magunguna. Tunda muka dawo gida yaya ke jinyata,Sallah kurum yake fita har abin da zanci shi ne ke girka min,, ya min wanka,abin ya kunna Mujidat har ta kai su ga fada ya mareta, tun daga lokacin ta yi wa kanta alkawarin kawo karshen zaman shi da matarshi ko ta halin kaka. Yayan da zai yi kwana biyu sai da yayi biyar ya ga nadan murmure,sannan ya tafi..
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Duk abin da nake so sai da ya tanadar min

isasshe sannan ya tafi. Kullum gidan ba ya rabuwa da 'yan dubiya. Aisha ta yi ta yi min iskanci wai na narke sai ka ce cikin fari, Yaya shi kuma ya daure min gindi tun da tazo ta ga yana ba ni abinci a baki shi kenan fa,nace na ji dai ai ko wane ciki na fari ne tunda wuyar dana ke ciki da wannan na fari ban sha ta ba.
Na rarrafa kicin ina dafa taliyar Hausa, sai ga Mujidat daga yawonta an zugo ta ta shigo da fushi, Mama tana wasa da abin kama shanyar ta da ya fado daga igiyar yaronta, ban ma lura da shi a gurin ta ba sai na ga ta kwace tare da rankwashin ta a kai tana zagin ta da Turanci. Maama ta yanka ihu raina kuma bace na ce mata. Ke! Na nuna ta da yatsa. Ki shiga hankalin ki, wannan 'yar yarinyar zaki doka? Wallahi ba zan dauka ba. Ta harareni tare da ce min ta doketa, kuma kada in ga wai nayiwa mijina asiri yana mata wulaqanci in dauka za ta tafi ta bar shi, to in sani ita fa ba inda za ta, domin shi kadai ta gani miji,sannan in shirya barin gidan bada jimawa ba. Na yi dariya. 'Ke ko Agumin ku yayi kadan bare ke, ba da tsafi ku ke takama ba? Mu zuba ni na riqe Allah.Ta shiga daki fuu! Na yi mutuwar tsaye ina mamakin lamarin,wannan ai ke ce kwarkwasa fidda mai gida a gidansa,iInshaAllahu ta Allah ba ta ki ba.
Haka muka ci gaba da zama cikin husuma kullum sai ta tsokaneni,in na yi kamar in hada ta da mijinmu sai in kyaleta. Ashe ita kullum aka yi saita kirashi a waya. Sai da ya yi wani zuwa yake min zancen wai me ya hada mu da Mujidat ne?nace me akayi, tace anyi wani abune? Ya ce, Eh tace kin canza yanzun kintsaneta, kiyi ta zaginta kina mata gorin bana sonta,in ko har hakane bazanji dadiba, domin batun ina sonta ko bana sonta tunda yanzun ita ma matatace bai kamataba. Yafa bata rai wai dole sai ya kare mutuncin matarsa,inzaiyi adalci ai nasan ya fi nuna so da kauna gare ni. Nayi 'yar dariyar takaici, sannan na ce, Tunda ka mance halina har ka yarda da batunta shikenan. Amma in har

adalcin zakayi kamataya yi ka tara mu,dama 'yan sanda da bangare daya suke aiki in sun ji ta bakin me kara ya isar musu hukunci? Ya yi shiru sannan ya ce, To muje falo a kirata, Na ce a'a a barshi ni nayarda na dauki nauyin zunubin.ya ce ni dai na ce ku fito falo.
A gabanta na maida komai kuma ba ta musa ba,baisan tana fita ba sai lokacin danace ina taje aka zugota. Nan fa ya zaro ido ina take zuwa? Na ce ga ta nan ita ta sani, hankalinshi ya tashi ya ce mata gurin wani take zuwa? Ta zaro ido wai a'a gurin yaren su ne, dama shi irin wannan auren haka kullum a yi ta zargin juna, nan na tashi na bar su suna ta masifarsu.
Kafin ya tafi sai da ya kafa mata dokoki har da na fita, amma yana tafiya ta sa kafa ta shure dokar,sabida jarabarta ma ni na lallaba na soma zuwa aikina, yara ko na kwaso su sai in kai su gidan Iya in bana gida bana barin su a gida.
sai dai wani abu da na lura da shi shi ne wata dinkewa tsakanin Yaya da matar shi Mujidat, duk da cewa bai canza min ba, amma ina mamakin sabuwar shakuwar in yana dakinta har wani zumudi yake yi,sannnan ya kan dauki danta ya fita da shi wani dare ma har saloon ya kai ta, ko da dai ya min tayin zuwa na ce a'a, sannan ya kan dauke ta da yara su fita shopping duk da dai ya kan min tayin zuwa,ce masa nake a'a sai sun dawo. Haka nan zasu zomin da tsaraba,abin yana ta damuna hatta abincin ta da yake cewa ba zai ci ba yanzun nadeshi yake yi. Wani zuwa da ya yi sai na yi niyar gwada shi ranar da ya dawo dakin Mujidat zai sauka sai na yi tuwon shinkafa da miyar Ogun, bakwai da wani abu ya iso gidan. Taliya ta dafa dama girkinta bai wucetaliya da shinkafa da miya ba, ga shi ta zabga uban attaruhu, ta saka wando da riga an je an wanko kai, dan ma ba wani gashi neda ita ba da na doki ake gayun, kuma ya hana sawa,da in ya dawo ni yake fara nema a ko yana dakinta, yanzun kum in dakinta yake can yake yada zangoi,sai daga baya sannan ya zo. Ina sallar Isha'i ya leko, sai kuma ya shigo

ciki ya zauna,sannan na gaida shi ya amsa tare da tambayar jikina na ce da sauki sosai, na kalle shi. In kawo maka tuwon shinkafa miyar ugun ce? Kafin ya yi magana sai wayar shi ta soma kara, da ya daga sai ya ce, Ya? Ina jin haka na san Mujidat ce, ko me ta ce sai na ji ya ce'O.k, gani nan, Ya kalle ni.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Mujidat ce take jirana muci abinci, na so cin tuwon amma yaya zan yi tunda girkin ta ne zai fi kyau mu ba ta hakkin ta ko? Raina ya sosu matuka, amma sai na danne na ce, Haka ne, na ga ai kuna ta dasawa. Ya kalleni, Kamar yaya? Na ce,gani na yi kana ji da ita. Ya ce, Lallai Sadiya,harma zakice haka yanda na fifita ki a kanta kuma ta hakura? Nayi guntun murmushi, Ni ba ni san ka fifita ni a kanta, na fi son ka yi adalci, ni na san dama duk zance ne da ka ke cewa ba ka sonta. Ya hade rai, 'Wannan wace irin magana ce? Kin san ai matata ce, batun ina son ta ko ba na son ta ki aje shi. Ya mike tare da fadin. Banason irin zantukan nan kowacce ta zauna a matsayinta. Ya fice abin shi. Na jima ban iyatashi ba, eh na san ba laifi ba ne dan ya nuna kulawa ga matarsa,amma abin da ke ban tsoro yanda na ga yana son hada matsayin da a da ya ce ni kadai ke da shi ya raba mana. Anya nan gaba Yaya ba zai bijiremin ba? Wata zuciyar ta ce haka wane shi, zai manta asirin da Allah ya rufa masa kuma ke ma ki ka rufa masa.
Da safe muka shirya da yara zan aje su a makaranta nima in wuce gurin nawa aikin,sai lokacin suka bude kofa muka gaida shi, sannan muka wuce. Ko a makaranta a ranar tunani nake ta yi in zan lura da kyau yanzun ma bai cika nema na ba sosai, ga zatona don ba ni da lafiya ne, amma yanzun na gane ba haka bane.

Da muka tashi na kira shi na ce zan biya gidan Anty Abida,sai cewa ya yi shi fa ya tsani wannan yawon,daga can bai ce in je koina ba, na ce to. Cikin kuka nake fadwa Anty Abida matsalata, dariya ta yi tare da cewa, 'KISHI ke damun ki Sadiya ga shi kin fada kin ce mijinki bai canza miki ba,dan ya nuna kulawa ga matar shi ya ci abincinta sun fita tare laifi ne? Na yi shiru. Ta ce, ko yana miki sababbin dabi'u? Na ce, Eh, to jiya dai da na yi masa korafin cewa yanzun yana sonta kinga yanda ya bata rai,yana ta fada. Ta ce, Kar kikara yi masa zancenta, ba ruwanki da harkarsa. Na ce to shi kenan,amma fa bai cika son Taliyaba ko na dafa sai na yi masa abin da zai ci,amma ita sai ta yi masa yayi taci. Anty Abida ta ce, Na ce miki babu ruwanki. Nace, Yanzun duk ba shi da laifi? Ta ce, Babu. Na ce, shi kenan. Tace ki kauda kai ga tunanin zai canza kiyi ta kanki da lafiyarki. Na ce to Anty shi kenan. Na nufi gida ina zaton sam Anty ba ta hasashi abin da nake hasashe ba.
Tsakiyar falo muka same su ya dora Abdul saman kafadar shi yana yi masa wasa, yara suka yimasa sannu da gida,su ka nufi dakin su,nima dai sannun nayi masa zan wuce yace, Abdul yana ta kallonki MY CHOICE. Na dawo na daga masa hannu tare da yin dan yake,nawuce dakina.Ina kwance kan gadona ya shigo baifi minti biyar da shigowa ba, Sadiya! Ya kira sunana,bayan ya zauna bakin gado, na amsa da na'am ba tare da na taso ba. Ya ce, Ni na ga kamar kin canza min? Na ce, Kamar yaya? Sai in ga kamar idanunki suna tuhumata a duk lokacin dana kalleki? Na ce, A'a kai ne dai ka ke zargin kanka. Yace,shikenan, ya jikin naki? Alhmdllh. Ya ce, To haka akeso.Yakai hannunsa ya shafi cikina,ya babyna? Ban tanka ba dan ni fa yanzun abu kadan ke bani haushi, ya juya zai fita kenan sai karar shigowar sakonni cikin wayata, ina ji na san daga facebook ne,na kai hannu zan dauka shi ma ya kai, saiya riga ni dauka, gabana ya fadi dan na san cewa ya ce na goge,ban goge ba. Ya dawo ya zauna, 'Sadiya.

'Na waiwayo na dube shi. Bana ce ki rufe wannan account din ba? Na ce, 'Zan rufe ai. Ya ce, ba kida niyya. Ya soma fada. Ni fa bana son taurin kai,wata nawa da cewa ki rufe,mekikeyi a internet?na ce 'Karuwa! Nima cikin zafin rai na fada,ya ce in ban da shashanci dubi yadda maza suke requesting dinki. Na ce, sai ka duba ka gani na yi accepting? Ya ce, Ina ruwana, na dai ce ki rufe kuma kin ki don haka yaune karshe, in ba ki rufe ba sai kin daina rike babbar waya. Zuciyata ta tunzuro na ce, O.K, sabida nice zakace ma haka, amma matarka da yake ita kana shakkarta ba yini take yi chatting ba? Ya ce, Ita ma tunina hana,ita da har wayar na amshe na ba ta karama me ta ce? Na dago na kalle shi, Har yanzun chatting take yi. Ga mamakina sai na ji ya ce, Karya ki ke, 'yar Nokia ce a hannunta,ina ruwanki ma in me take yi? Ke dai ki hanu mana da abin da na hana ki? Ke yanzun kin kama taurin kai,nema kike ki canza hali ko? Kinfi son a yi ta fitina? Fuu! Yafice abinsa. Sai na samu kaina da jin zafin kalamansa,kuma na dauke su a matsayin wulaqanci da tozarci,wata zuciyar tace me yasa tuni da ya ce ki rufe account din kika qi? Ina kokarin amsa laifi na ne sai wata zuciyar daga gefen hagu tace shi ne zai fadamiki kalaman batanci har da kiran ki shashasha? Bayan ita waccan tana yin chatting ma bai hana ta ba har da cewa karya ki ke mata, to kema kar ki rufe duk abin da zaiyi yayi. A fili na ce, Ni da nake karanta abubuwan karuwa a ciki ma ba zan rufe ba.

Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Har ya tafi sama sama muke, amma duk da haka yana kiran wayata sai dai ba na iya yi masa hira dan haushisa. Tabbas in ma ya hana

Mujidat hawa internet to tana yi a boye dan tana yi a gabana, sannan ba ta daina zuwa gurin yarensu ba. Ni kam yanzun ba abin da zai fi min illa in yi watsi da su in yi ta kaina. Kwanci tashi cikina ya shiga wata na biyar,na dan gyagije daga laulayi,kuma na soma siyayyar kayan babyna. Tabbas Mujidat tana jin haushin cikina,don ina lura da irin yanda take yawan zabga min harara, sannan in ba ni ce na yi mata magana ba itabata yi mini. Haushin da take ji nawa a yanzun ko da da yayan bai damu da ita ba ba ta ji kamar yanzun. Wata Litinin na dawo daga aikina tare da yarana, na kai minti biyar ina buga gida ba a bude min ba, har nasoma zaton ko ba kowane a ciki, sannan aka zo aka bude, sai dai wani rainin wayo ashe suna zaune a harabar gidan ita da wadanda take zuwa gurinsu su ma yau sunzo gurinta. Cikin fushi na kalleta. Maman Abdul kina nufin zamanku a nan bajuji duk bugun gidan da nayiba? Ta yatsina fuska, Na ji mana ba gashi na bude mikiba? Na yi kwafa tare da juyawa na nufi ciki,sai na ji sun yi wata magana cikin yarensu,sai kuma suka kwashe da dariya, na dawo baya cikin zafin rai na ce Maman Abdul ki ce da mutanen nan su fita,tace yazakice su fita,wurin ki suka zo? Na shiga kicin na dauko muciya nanufe su. Ku fita daga gidan nan maza maza.Cikin sauri suka fita suna yare, itama tabisu, na maida gida na rufe, na koma ciki, ina ta huci. Hatta su Kausar sai kallona sukeyi tamkar na zamar musu sabuwa. Kusan awa daya na ji tana buga gidan, banza na yi da ita har Al'ameen sai da ya zo ya ce Momy ana buga gida, shi ma na kore shi, kusan minti goma waya ta ta soma ruri na gane Aliyu ne, dan ringing din shi daban ne, na daga raina a cushe,ban raini shi yasa dukwanda ya yi min raini nake jin zafi. Ya ce, Sadiya yaya za ki rufe mata kofa, ki bar ta a waje? Na ce, Wa? Ya ce, Au! Ba ki ma san kowace ce ba? Bari ki ji Mujidat fa matata ce kuma ina son ta kamar yadda nake sonki tayaya zaki hana ta shigowa

gidana, duk rigimar da kukayi dai ai kin san ba ta da inda za ta. Zantukan shi suka zafafa zuciyaa,sai kawai na kashe wayar, yayi ta kira na ki dagawa,can sai ga kiran Anty Abida, ta soma min fada wai me yasa na canza, mijina da ke yabona ya koma korafi akaina. Na ce, Allah, Anty ba zan bude ba, ni za ta maida 'yar iska? Shi kuma dayaji ta bakinta baya tuntuba ta, sai kurum ya kira niya fara masifa, nagaji, shi kanshi fa ya'isheni ke! Anty Abida ta katse ni 'Kina hauka ne za ki ce mijinki ya ishe ki? Shi kuma wannan cikin da masifa ya zo miki? Ki bude mata gidan ta kira shi ta mafada masa, ya kira ki kin ki sauraron shi shi yasa ya kira ni, nima ba ki saurare ni ba? Shiru na yi mata tace, Shi kenan. Ta kashe wayar, ni kaina ina mamakin kaina yanda zuciyata ke ta tafasa.Kamar daga sama su Kausar suka ce Momy ga Iya fa. Na buga kafa,ashe shi ya kira Iyan ya fada mata, jikina na rawa na je na bude, ta kalleni ranta a bace. Sadiya lafiyar ki kuwa? Yaya za ki koro abokiyar zaman ki waje ki kulle gida? Na kalli Mujidat wadda saboda makirci har da yin hawaye, na ce,Iya akwai abin da ya faru. Iya ta kalleta jeki dakinki kinji? Na soma kuka. Yaya za a ce kowa ba zai tambayi ba'asi ba sai kawai a yita ganin laifina? Iya ta ce, An gani, sakarya, a gaban kishiya za ki yi kuka 'ya'yanki suna kallon ki. Fuu! Na juya na nufi daki raina a bace, ina gunjin kuka, Iya ta biyo ni cikin daki tace, Sadiya yaushe ki ka zama haka? Na ce, To, ni Iya shi kenan ba wanda zai tsaya ya ji dalilina? Ta ce, Eh, ba wanda zai ji ke bake ce babba ba? Ko me ta yi miki sai ki tura ta waje? Me mutanen unguwa za su dauke ki? Na ce, Wallahi Iya ni ban tura ta waje ba, ki fada mata ita ma in na buga kofata ringa bude mini. Na kai minti biyar ina buga kofa suna wurin sunki bude min, da ta ga dama ta bude na yi mata magana nace meyasa ta barni tsaye ina ta buga kofa ga yara ni kaina na gaji fa, sai ta ce min wai batajiba. Na tafi kuma suka yi min dariya suna yare, ni ko na cewa wadancan su

fita shi ne ta bi su ni ko na rufe kofa. Iya ta ce, shi kenan zanyi mata magana,amma kema ki dinga tausan ranki dan naga kina fama dazafin rai,ina zaton kuma ciki ne ke saki saurin fushi. Na ce ko ba ciki dole inji haushi,Shima yaya ba bincike ya kira ni yana ta min ihu shiga mai mata,har da fadin cewa wai gidan shine, to ina ruwana da gidan shi? Na soma sabon kuka, Iya ta ce ki yi hakuri zan yi masa bayani, na san cewa har da ciki wannan saurin fushin ki dinga yawan salati kin ji? Na turo baki nawa ganin sun dai ki fahimtata ne, na ce ita ma ki gaya mata fa? Shi ma ki gaya masa. Ta ce zan fada musu. Ta dinga tausa ta har zuciyata ta sauko sannan ta tashi na raka ta,ta shiga dakin Mujidat ni kam na yi bakin gate jiran ta.ta iso ta ce na yi mata fada ita ma,don haka a zauna lafiya. Na ce to Iya na gode, da na rufe gidan na dawo sai naga Mujidat ta shiga kicin tana kumburi,nima na yi cikin dakina. Iya tana isa gida Aliyu ya soma kiranta,sai da ta zauna, sannan ta daga wayar ta ce, Na dawo ai ta bude mata,dama ashe ba ita ce ta koro ta ba. Ya ce, Ita din ma za ta iya saboda yanzun Sadiya ban da neman fitina ba abinda take yi, shi yasani yanzun ko son zuwa Kaduna banayi. Iya ta ce, Ita ma Sadiya ba laifinta ba ne kowane da irinsa,kuma ba sabon abu ba ne kowa ya san mai ciki da saurin fushi. Ya ce Iya ba ruwan ciki kada ku goyi da bayanta, na soma tunanin damar dana bata ne take zuwa koyarwa,can ake zugo ta, don haka in na zo zan soke. Iya ta ce, Kull Ban yarda ba,ba abin da ya shafe ka da batun aikinta, ka dai yi hakuri har ta haihu,kuma wannan rikicin tsokanar ta Maman Abdul din suka yi ita da yaransu, shi ne ta kori wadancan ita kuma ta bi su. Aliyu ya ce, Amma da na kira ta ba sai ta fahimtar da ni ba, shi ne zata tsaya yi min taurin kai? Iya ta ce, Na dai kashe wannan wutar zancan kuma ya mutu.Ya ce shi kenan.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com

Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Goman dare ya kira ni na daga ciki ciki muka gaisa, ya ce ranar Litinin zai turo da kudin abinci, na ce muna da abinci mai ne da su maggi ya kare, sai Indomie.
ya ce to bayan nan ba wata natsala? Na ce babu, sai kudin asibiti zan soma zuwa awo,sannan sai kudin siyan kayan baby. Ya ce to na ji nawa zan bada? Na ce to ka san dai komai sai na siya sabida bakamar na Mama ba da na yi amfani da wasu abubuwa na Al'ameen. Ya ce, Ni dai kudin na tambaye ki, Na hade fuska kamar yana gabana. Na ce, Dubu Hamsin. Ya ce,hamsin? Na ce, Eh, kila ma ba za su isa ba,in kuma in bari sai ka zo mu je to. Ga mamakina sai na ji ya ce, Me yasa haihuwar Abdul ba a kashe wannan kudin ba? Wani bakin ciki da takaici da ya zo min wuya, kawai sai na kashe wayar, Ina jefar da wayar yana sake kira, na daga ya ce, Lallai na yi kuskuren barin ki ki fara koyarwa, daman can kika koyo sababbin dabi'u kin rainani, ba ki da buri sai ganin nuna husuma, to zaki dai na koyarwar in ga tsiya. Duk da qoqarin da nai in danne maganar,ashe ta fito,sai kawai na ji na ce, Sai me in daina mana? Ya ce, Iye! Lallai kin rika ba laifin ki ba ne nawaa ne da na kira ki. Sai ya kashe wayar. Sororo na tsaya ina kallon wayar zuciyata tana ta yi min fadan cewa ban kyauta ba, mijiki yana son kyautata miki amma na kasa yin abin da ya dace.Hawaye ya soma zuba a idona,na dauki wayar da nufin in ba shi hakuri,amma sai wata zuciyar ta ce da Allah bar shi ya karata. Sai ko na yi tsaki na share.
Allah sarki ranar Litinin ina zaune tare da Malamai kawaye na muna hira,sai ko na ji shigowar sako,ina dubawa sai na ga alert ne dubu sittin kamar minti goma sai sakon shi ya shigo kurum cewa ya yi goma na asibiti,tausayin shi ya kama ni. Tun ranar damuka wannan

husumar ba mu sake yin waya ba,don ya ki kirana,take na soma kiran layin shi amma har ta katse bai daga ba,sai na ji haushi tare da jan tsaki. Da na koma gida ban samu Mujidat ba duk zatona tana can gurin yawan gulmarta,sai na ga har dare bata dawo ba, duk da cewa ba ma shiri sai naji na damu,na kira Iya na fada mata,ta ce ina ta je? Nace na dawo bata nan. Ta ce to duk inda ta je ta dawo,tun da ba yarinya ba ce. Wasa wasa har washe gari nakasa hakura na kira shi ya ki dauka,sai na tura masa sako cewa Mujidat fa ba ta kwana a gida ba,don Allah ya kira ta ya ji in da take, dan ba ni da lambar ta. Kamar mintibiyar sai ga amsa. Kar ki damu muna tare. Shiru na zauna ina nazari, har mun zo lokacin da Yaya zai min haka? Nan na kira Anty Abida da kuka ina karanto mata komai,tun daga wancan rigimar da muka yi ta kudi zuwa yau. Ta ce abin da yayi shine daidai ya barki kici masifarki. Cikin kuka nace, Kunki fahimtata. Tayi tsaki sannan tace, Tunda kin rika har kina rigima da mijinki sai ki yi ta yi. Ta kashe wayarta. Na yi dogon tunani don in gano laifina,amma kwanyata ta toshe,don haka sai na watsar.
Kwanan su goma sai ga su ta zo tana ta isa da bunkasa,ita ga 'yar gaban goshi. Allah ya taimaka ranar zuciya ta sumul, na musu sannu da zuwa har da ba su abinci, su Kausar suka soma rige rigen daukar yaronta,don in bana nan ya kan basu shi, duk da cewa ita bata so,daga nan na koma dakina na kwanta. Shi kan shi bai zaci zai gan ni wasai har in kalle su ba. Ya shigo, Ya jiki? Na ce ba inda ke min ciwo, ya ce kin je Asibitin? Na ce eh, Na nuna masa kayan da na siyo na baby na ce ga kayan can, ya kalla. Allah ya raba ki lafiya. Na ce amin. Ya ce,saura wata nawa? Na ce, Eh to, EDD dinasunce watan sha biyu ne, yanzu kuma muna watan tara,saura wata uku. Ya ce, An kusa, ina san nema in canza gadajen gidan da kujeru,tunda na samu na sai filin can.
Na ce, Au har an siya bamu da labari? To Allah

ya sanya alheri. Da sauri ya ce ta waya muka yi komai na tura kudin ta banki ko Iya bata sani ba tukunna. Na ce, Allah yasa alheri. Ya ce ameen. Can kuma sai me? Ya ce, Nasan na miki laifi na kira Mujidat bada sanin ki ba....... Da sauri na daga masa hannu, Yaya dan Allah duk abinda ya shafi batun matarka bana son ji sabida bana buqatar bacin rai, don bana son in yi wata magana ka yaba min baka Matarka ce ku karata.sai na mike na bar dakin zuwa falo na zauna. Aikuwa washe gari ya tafi..
Yadda akai Mujidat ta tafi Abuja kuwa, tsohon saurayinta mai nacin sonta wanda ko yaushe suke yin waya, shi ne ya fada mata zai shigo Abuja tayi kokari su hadu mana. Aminiyar ta Murfat ta dinga yi mata famfo ta je ta shirya mata yanda zasu hadu.Don haka ta kira Aliyu cikin kukan ta wiwi, yatambayeta dalili sai ta fada masa kewarsa ce ta dameta, yaushe zai zo? Yace bashi da rana domin yawan rikicin su ya isheshi. Ya ce, Kin cika tsokana da mata ta ba ruwanta amma zuwan ki kin maida min mata mafadaciya. Ta ce, ba ruwa na kishin matar ka yayi yawa, alhalin kuma ba ta kaini son kaba. To yanzun ya zan yi don bazan iya riqe kaina har zuwa wani lokacin ba. Ya ce, to ki taho gobe zan zo in dauke ki,za muyi tayin waya har ki iso.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Ranar da ta cika kwana hudu a can ne suna cin abinci wayar ta ta soma ruri, ya fi kusa da wayar don haka sai ya dauka, Uncle ya gani an rubuta, ya ba ta ta dauka da murna ta ce, Uncle yaushe za ka shigo Nigeria? Ya ce, Bakiga lambar da na kira ki ba? Ina Nigeria ai, ina Abuja. Ta fara ihu ai ita ma tana Abuja gurin maigidanta, ga shi ma su gaisa. Aliyu ya amsa suka gaisa,amma shi sam bai ji abin ya shige shi

ba, yana jin su har ya yi mata kwatancen inda suka sauka, Aliyu ba inda bai sani ba, don haka ya ce ya gane gurin,sai dai ba za ta ba, ta dinga rokon shi wai kanin Mamantane da ke zaune a Germany,sun dade ba su hadu ba. Da kyar ya yarda gobe zai kaita. Washegari ya kai ta dakin shi har suka gaisa da shi da wata da ya gabatar masa wai iyalinsa ce, nan Mujidat ta rungumeta tana fadin, Anty. Shi kuma ya dauki Abdul yana nuna murna da ganin jikanshi a cewar shi, har ya kara da cewa yaron ya biyo jinin babanshi. Aliyu ya ce to za su tafi,sai wanda yake amsa Uncle din ya yi rokon shi kan cewa ya bar su su yini. Da kyar ya yarda. Mujidat sun lalace da saurayin ta yini guda, hankalin Aliyu ya kasa kwanciya don haka uku daidai ya bar komai ya nufo gurinsu,sam ba su zata ba sai dai an yi sa'a sun fito falo suna hira,ya diro ya ce su fito.sun fito, nan ya shaka mata kudi masu yawa,sai dai dubu goma ta cewa Aliyu ya bata. Bayan dawowarsu ne ta yi ta siye siyenta har ta sai wayar da ta siya a boye tana chatting, ta ji dadin zaman Abuja rayuwar da suka yi ta kwana goma da mijinta, da ma ta fi so daga ita sai shi da dansu. Don haka ta sha alwashin duk yandaza ta yi ta raba ma'auratan dan ganin cewa ita kadai ce ta mallaki mijinta. Lokacin ni kuma na shiga zargin cewa shi ne ya ba ta kudade,ta je gidansu Anty Ramatu gidan da kullum take zuwa, da yake sun fi shiri da Ramatu, sabida ita ce mai zuga ta a kan kishiyarta, ta ce mata Hausawa mugaye ne in ba ta yi wani abu ta kare ta ba, to ita za takoreki. Mujidat ta ce ina Yusufu? Kanin AntyRamatu kenan. Ramatu ta ce, Yana dakin shi. Mujidat ta je gurin shi ta ce, Yusuf ya maganar mu? Yusufu ya ce, Anty ai ke nake jira mun gama magana da yaron Bahaushene, kudi kawai yake so. Tace, Ko nawa ne zan ba shi. Ya daga waya 'Bari in kira shi. Yaron ya zo, jamilu sunan shi ya san kan computer sosai, hatsabibi ne. Mujidat ta ce ina son a hadawa wata mata sharri ne ta hanyar internet, yanda mijinta zai rabu da ita. Jamilu ya

ce ita ma tana hawa internet din ne? Mujidat ta ce tana hawa,kuma mijin ya hana ta amma har yanzun ina ganin ta.Ya ce tana saka hoto? Mujidat ta cea'a, ya ce kina da hoton ta? Mujidat ta ce a'a. Ya ce, To ba matsala nawa za ki biya ni?Zan baka dubu uku. Ya ce, A'a ki ba ni biyar, cikin sati daya zan ba ki mamaki. Ta ciro dubu uku cikin 'yar jakarta ta hannu (post) ta ce, Rike wannan zan cika maka in har ka yi min wannan aikin da kyau,sannan duk lokacin da irin haka ta taso zan yi maka magana. Ya ce, An gama. Nan take ya bukaci ta fada masa sunan da matar ta bude account din ta, ya kuma ce ko ta san wani da matar ta sani? Mujidat ta ce a'a,sai dai tana koyarwa a primary. Ta yi ta yi masa bayanai a kan Sadiya, sun rabu a kan cewa zai turo mata duk abin da ya hada a nata account din ta gani.
Kamar an jeho shi ina kwance a tsakar dakina, sabida kowa ya san mace mai ciki da jin zufa, har bare ana cikin yanayin zafi. Ya tsallaka ni na dago kai cikin faduwar gaba na ce, Lafiya Yaya? Wayar da ke gefena yasa hannu ya dauka,sai huci yake kamar kumurcin maciji na yunkura na tashi zaune, ina sake cewa. Lafiya Yaya? Ya dubeni idanunsa jajir 'Dama duk tsawon lokacin da na ce ki rufe account dinki na facebook baki rufe ba? Gabana ya yi mummunar faduwa,sam na manta da shi, banama hawa. Na kalle shi. Kawo in rufe wallahi ba na ma hawa kuma na manta ne. Ya soma sintirin kai kawo a dakin,sannan ya ce, 'Kin ba ni mamaki Sadiya in wani ya fada min ba zan yarda ba..............
Abin tsoro sai na ga hawaye sun soma zuba daga fuskarsa. 'KINA BIN WANI SADIYA, DA ME NA RAGE KI, KI KE BIN MAZA??? KASH! Kash amadadin HALIMA ABDULLAHI K/MASHI. Ni ANaM Dorayi nake cewa dan jin yaddaza ta kaya mu hadu kashi hudu wanda ya fito tare da na ukun nagode,dan Allah inna barar addu'inku Allah yayemin damuwar dake cina,kwarrai inna cikin damu.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai

masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Zaharaddeen Shomar
Whatsapp 08168575100